Shikenan k'adara da lefin zina da Mama da Abduljab sukayi a kaina ya sauka  Insha Allah bazan je garesu ba na lalata musu  jin dadi su  ba Insha Allah  zamu hadu a lashira

Shiko Baba yana kara sawa bedroom din shi yayiwa Mama kiran gaggawa  kafi tazo har ya har giza dakin tun daga kan zanin gado da komai na bedroom din yana kuka idon sa yayi fulufulu dan saida yajima yana kuka sannan ya kirata yana jin ta murda kofa yafara buga kansa a bango  yana kuka wuwu
Da sauri Mama ta karasa inda yake a tsorace ta fara tambayar meya faru dan koda kuwar da uban sa suka mutu baiyi wannan kukan ba

"Alhaji lafiya shikenan an haukata min Kai dama shiyasa nasha kawo maka magunguna na kari ya yanda ka daukaka aduniya ai dole kazamu makiya wayake zama haka yanzu amma baka son amfani da magani  aiko ba asiri akwai bakin mutane ."

"Kingi Wllh kwara hauka akan abinda yafaru Dani."
Tace
"Alhaji meyake damun ka haka kaduba tsawon wata hudu Kenan ko 5 ka haram tamin kwana a dakinka kana cikin matsanacin damuwa amma ka kasa gayamin Wllh ba banza bane muje wajen malam yaduba ka sosai."

Tasowa yayi yana kuka ya fada jikin Mama yace
"Kingi ayanzu rayuwata bashida amfani ko ba akashe niba ni Zan Kashe kaina dan idan kika ji abin da yafaru ke kanki zaki zabi mutuwata fiye da rayuwa na dan naci amanan matata Kingi

taya bazan gujeki ba tsawon watannin bayan amanan ki yana cikin fushe dani."

"Wllh Allah kome kayi bazan gujeka ba."

Sake fashewa yayi da kuka itama haka suka hadu suna kukan sosai
"Alhaji idan baka gayamin ba zaka shiga hakkina."

Tashi yayi yana cigaba da kukansa ya dauko laptop din ya kunna ya ajiye yakoma ya kifa kansa da bango yana sauke ajiyan zuciya

Itama Mama kanta wani irin juyawa kanta yakeyi wani wawan nunfashi taja ta zube sherkaf
Juyowa yayi yace "au tafiya zakiyi shikenan na jefi tsutsu 2 a dutse daya
Har zai fashe da dariya yatuno da ma k'udan dukiyar da yake hannun Mama wanda harkan awaje takeyi bai san sirrin sa sosai ba afili yace Khadija ba yanzu zaki mutuba da sauran likaci da sauri yayi inda Fridge yake ya dauko roban ruwa ya kwara mata taja nunfashi idon ta arufe amma hawaye yana surtowa a hankali bakinta yake furta astagfirla Allah lefin da nayi sama da shekara 24 sai yanzu hukuncin YA haukaina y'ata ta cikina ita take neman mijina Ashsha kincuceni wanda ya gaya miji cewa ke shegiyace shima ya cucemu yazanyi da wannan kazantan acikin gidana...

Baba yace "kuma kinsan abin tashin hankalin ma wai ciki ne da ita na tsawon wata 4 tace,
Ban yarda ba na tambayi doctor Abbas yake cemin ai jiya ta ce amma yace za a iya zubar da cikin cikin sauki batare da asiri YA tonuba,
Amma Kingi kiyi hakuri bazan iya rayuwa ba zan mek'a kaina a jefini kawai."

Alhaji hakan bazai yuwu ba dan bazan yarda akan wata gurbataciya na gurbata sauran yarana ba idan maganan nan yafito asalin yarana zan bata dan haka ita guban ita yakamata tabi duniya."

Afirgice ta fito

Tura kofan Ayyya tayi tazubawa Ayyya da ta zama kamar wata mutum mutumi dan jin komai nata jitake baya aiki

"Aisha Sai Yau nayarda sin taccen mage bata mage lefin ki ya girmi duka ya girmi zagi Saide nace miki jeki kyagani,
Mu muka rufa miki ariri muka rayu dake bamu gayamiki asalin kiba shine kika bincika kika sani idan dukiyar kike so bata haka ya kamata kikar ba ba akwai hanyoyi da dama cikinsu harda kisa dan da kashemu kikayi yafi da wannan tozar cin ai mutuwa gidan kowa awai amma banda kazanta irin wannan ki gaggauta barin gidan nan kuma duk inda zaki je kar ki tsaya akusa kije inda mudake Sai alashira zamu hadu ga wannan ATM din akwai kudi da zaki iya rayuwa a duk k'asan da kike so ki tashi nace tun kafin gari yagama wayewa."

Murmurshi Ayyya tayi tace ai ko baki koreni ba nima bazan zauna agidan dabbobi ba amma yazanyi da cikin Mijin ki ko kunbar min?

Dafe kirjinta Mama tayi yanda yake mata zafi
tace "Al dama ke kika sashi yayi adole ki tafi dashi abinki ba ma bukata ke ma ki kayi mana haka balle wannan cikin naki da yafi shege shegan taka ai yafiki goba."

"to Mamata kishiyata naji dukiyata fa.?
Kudin da yake cikin ATM din nan yayi Rabin abinda kakanki yabaki so ya isheki mukuma zamu rike sauran dan muna da hakki akai."

"Kai Mama bakuyi cuta ba kituna canjin da dana yanzu ba daya bane."

"Wllh Ayya da dayanda zanyi da nabaki dukiyar duka yin hakan tonan asirine ne kije ya isheki."

"to mama kafin nafita ina son nasan address din dan tauren saudia da kukayi cikina."

Ido Mama ta zaro "Dan taure kuma."

"Eh mana Mama Al ke yar akuya ce wazaki bi inba taure ba."

Gigiza Kai mama tayi tace "Ayya nayi na nadaman  haifuwan ki."

"Kai Kai mama ai sai Yau kikayi Nadama ai azatona tun da kikasan kina da cikin zina ki kayi nadama amma kin makara wajen nadama."

Gigiza Kai mama tasake Yi ta fara Jan kafa zata fita da gani tana cikin matsanacin damuwa
Sai da taje kofan daki tajuyo tace Ayya idan kika kara mintuna 15 acikin gidan nan zan zuba fetur na Konamu duka kinga an futa."
Tafita

To ni kuma abinda yasa na fita bana son ta kona ma aikatan gidan wanda akallah sunfi mutum 13  kuma nasan tunda tace zatayi zata iya  shine na shirya a gurguje na dauki ATM din nafito ta kofan baya
Na zauna a bayan gida sai da asuba  na bara tafiya akafa nazo Tasha  inda muka hadu da Hamra

Suka fashe da kuka dukan su ukku

Shi kansa malan hawaye yake
Yace "to ina shi lawyer din naki meyasa baki ne meshi ba.?

Al nabar wayata adakin Modu a lokacin amma yanzu muna tare dashi yayi yunkurin aurena

mama shi ta hana  dan labarina ya baza barno da temakon Baba Duno shine ya baza komai Amma shi *Geerem* bai hakura ba yana zuwa yabiyawa kansa bukata yakoma a kaina yafara zina."

Malam ya girgiza Kai yace to ya batun HIV kuma yakikayi dashi?.....

*Kunga labarin Ayya  amma naji comment dinku itada Hamra waya fi taka kaddara me zafi kafin azo kan oganniya  Ruwaida*

*B JATTKO*
[9/17, 11:11 AM] Batul Adam Jattako: AMFANIN SOYAYYA*

*NA*

*BATUL  ADAM  JATTKO*

*SIS kuyi hakurin rashin gani na online wayan ne yasa mu matsala amma zakuci gaba da ganin Post a wayan sis dina  nagode da kulawan ku*

*Kunbane dariya a comment dinku fa to de damasu cewa rayuwan AYYARAM yafi tada hankali da masu cewa na    HAMRAT duk naji amma nide RUWAIDAT ce tawa* 🤸🏽‍♀️🤝🏻

Kainuwa Asso🤝🏻

*7*

"Bani da HIV munje gwaji yafi a irga ana cewa bani da shi,
To saida nasamu shi doctor Abbas din dana hadu dashi a instagram na tambayeshi yake cemin ai baiyi amfani da asalin kwan masu HIV din ba asalima nashida matar sa ya dasa yaturomin pic nayaran sa sak Barrat   yanzu haka rigima ne sosai tsakanin sa da matar sa wai sai ya karbo mata y'arta dan ita maza ta Haifa shikuma yana tsoron tunkarata ne  amma inajin har takai zancen har kotu wanda ni hakan yamin daidai dan andauko hanyar tonan asiri kenan duk da nasan bawani nasara zata samu ba Dan da alama alkalin Baba Duno ya siyeshi."

Malam yace "yanzu dukka Dukiyar Alhaji Dunoma na barno nakine?
Yanzu duk tsoran Allahn mutumin nan da yawan shidim tawa addini zuciyar sa ba mekyu bane?
Yaki yarinya yakira BARRAT da take faman Game a wayan Ruwaida  shikuma Abdullah  a wayan Hamrat ajiye wayan Barrat tayi ta karasa wajensa Shafa kanta yayi Yana mata addua Yana aiyana Allah yasa su Ruwaida su shiryu kafin girmanta dan Barrat ba baya bace a kyu
Ya dago ya kalli  Albdallah yace "yaka Yaro shima Shafa kansa yayi yace "shikuma fa."?

Hamra tace wannan shine Abdullashi  wanda zaka jishi cikin rayuwan RUWAIDA."

Malam yace sunan medadi da ma ana Ruwaidatu  sunan ake kiranta da RUWA  AI da bangane ba  da alaman gaskiyar sunan AISHATU SADDEEK'A ko dan tafi kowa yawan ruwayoyi acikin sahabbai mata me sunan Aisha ake kira da Ruwaidatu."

Ruwaida tace" hakane gafurta amma ni labarina dogo ne wanda Yana bukatan zama na musamman gashi Rana yayi."

"ba damuwa ya Kalli dan agaji yace shiga da yaran nan ciki a basu abinci nima zandan sallami wasu awaje tare malam da dan agajin suka fita ya kama hannun yaran kirane yashigo
Wayan Hamra wanda tuntuni anakira yana silent kaninta Wasslim  ne dauka tayi tana cewa" cikin ummuna  ya akayi ne."?
"Aunty fine akan maganan masu neman auren Juwai ne  gobe zasu zo Shine gaskiya bana son sarakan bakin cikin nan su karbi mutanen shine ko zuwa zanyi ne
Wllh banason tarasa wannan daman a karau na 6 dan muddin Baba bazai dena sa Nura cikin rayuwar muba bazai tabs yin  kyau ba."

."dan uwa kwantar da hankalinka komai yazo karshe basai kabar aikinka kazo ba  kasan turawa basa son wasa da aiki zamuyi shawara da *Sahal*
wai wata fitar ne."?

Dariya wassilim yayi yace "AI kinsani *Akkaram  Shiddas* mana."?
"bawani Wannan zabin kane saboda kana neman aure a gidan ko."
"ni kuma ANTY AI ambani Ammatee fahtiha kawai nake jira
Ita kuma Juwa AI kyu da asali tagani."

Dariya Hamra tayi tace kaide fadi gaskiya Fulani atare a barebari amma kasan duk kwa nan ka Sai nabaka Barrat idan lokaci yayi dan ba abinda wannan kajerar zata nuna mata gata kanuri itama."

"haba  AI ko alahira angel ta ishini."

"AI shikenan muma me zamuyi da second ai  ga Habibullah."
Yace "shike nan ma futa roro
kibawa aunty ruwa."
yace
Daga nan suka shiga fira da Ruwa  dan Wassilin yazama goggegen Dan Boko yana aiki a London  babban abokin sa  Akkam Shid shiyaba shi aiki a companyn su  dan kannen Hamrah sun samu karatu mekyu  dalilin haduwan Hamrah da SA IDU WALWALA Dan kidan tsohon mate makin shugaban kasa wanda ta taba haduwa dashi a secretariat  shi yaje makarantan su Wassilam da Sunan yana da kokari gomnati ta dauki nauyin sa da ganan yanemi sanin iyayen sa yatemaka musu sosai   dan family  Kabir Sankira abinda Nura yamusu ya zame musu

hassada game rabo Dan yanzu kabiru kurma da Dumba sun zama Alhaji da Hajiya amma basu san dalilin Hamra yake musu
ba hassadan gidan Sai abida ya karu idan anzo neman auren Juwairiya su suke cewa Al Karuwace ce dan a mazan da take bi aka samu Wanda ya dauki nauyin su dan yayar tama haka tayi Sai afasa auren gashi de yanzu ta samu ko yaya zai kasance

Bayan malam ya shigo

Labarin Ruwaida
Sunana AISHA MUKADDAM ME KWANO...
atsorace malam ya dago ya kalleta fukkan sa da alaman rashin yarda

yace "Me kwano ke medin sace.?

Y'arsa ta cikin sa."
Afusace Malam yanuna musu kofa yace" get out
Ashe dama duk labarin da kuka bani tasuniya ce yaudara ce irin naku na karuwai."
Mukaddam bashi da d'a bai taba haifuwa ba ko shekaran jiya anyi fira dashi a news bai taba haifuwa ba dalilin hakan yaje gidan marayu ya dauki yara 2 da sunan zai rike kuma tunda ma ansan Mukaddam bai taba haifuwa ba zancen banza."

Murmurshi Ruwa tayi tace" nasani haka yake cewa tun da aka haifeni
Amma inason kabani mintuna 10 kacal nasan zaka yar ni yar sace ta nuna Abdullah tace Al ko fuskaan yaron yaci ga gane Yana da halaka da Mukaddam kuma yan biyun da yace marayu ya dauko suma Yaran sane halak."

Malam yajuyo Yana kallon Abdullah sosai yaga baiwar kama duk da Yaro dan shikara5 ne kuma shi malam bai taba ganin Mukddam ido da ido ba
"ina jinki."
yace amma har yanzu bai yarda ba Yana DE son jin nata batun

Alhaji Mukddam yayi aure da matar tafari Malam Hajara Hajara hafizar Qur ani ce sosai tun tana y'ar shekara 12 tayi sauka ta haddace hadisai da dama tana da mutukar kokari hakan yasa ta tashi da wani mugun farin jini a cikin garin kaduna iyayen ta talakawane sosai gidan da suke ma nahayane a anguwan hayin rigasan dattawa duk wani gasa na karatun Qur ani amakaran tansu to Hajara dattawa ce akan gaba kuma babu Tan Tama zata ci Alhaji Tashiru Mai Gwano tunda aka gaiyaceshi wani gasa yaga nusuwar Hajara da baiwan ilimin yayiwa dan sa tilo Muddama sha awa yasamu malamin su yagaya masa bukatan matsayin Tashiru Mai kwano aduniya bawani abinda zai gagareshi aiko ba adau lokaci ba akayi auren lokacin ma shi Mukaddam Yana waje yazo de yaga yarinyar kuma yace tayi masa Saide Mukaddam tun yara yaro yatashi da zafin nema wanda dama acikin dukiyar yatashi iyaye da kakani sun Gaji kudi amma baye Muddam bashida wani lokaci sai na nema Ya iya juya kabo yazama naira juya goma yazama ashirin acikin kan kanin lokaci ba wani Abu bane awajen Mudda bashi da lokacin

mata ita kanta matar tasa Hajara Sai da uwar ta Hajja ta matsa sannan yazo dama agidan su aka ajiyeta dan Hajja cewa tayi baza ta kaita ko ina ba suna tare tunda Mudda ba mijin zama bane a daddafe yayi kwanaki sa 10 da zai tafi Hajja tace yatafi da matar sa aiko bai musa ba amma yasan shi ko a can ba mazauni bane ahaka ya dauki Malama Hajara yatafi da ita aiko tayi nadaman binsa abin kida ustaziya acikin turawa haka tace ida zata koma Mudda bai soba dan yana mutukar son Malama tana tunatar dashi addinin sa sosai yana son zama da ita amma da yake shi bature ne bayaja da ra ayin mutum Sai ya aikota

Zaman kaduna yafi yiwa malama dadi dan sawa tayi aka gina mata islamiya acikin gidan tana koyarda matan aure da yan mata malama Hajara maccece da ake girmamawa ta Shara wajen fad'akarwa a kulmu cikin shidiman addini taken bude makaran tona rijiyoyin ruwa a anguwan nin masu karamin karfi gina masaltai a Sabin anguwani da k'auyuka kaiwa ziyara gidan marayu da asibitai Sam abin hannunta bai rube mata ido ma hakan ya tsayo mata kima da daraja a wajen dan gin Mijin ta musamman sirikar Hajja da Ahj Dashiru acewar su ta karawa family daukaka sosai ba kananun kudi Hajja take samu awajen Mudda ba kusan duk sanda taga dama tana ciran abinda take so ga arzikin Muddda wani Irina bungasa yake wanda yanzu duk duniya ansan Mai kwano shine dan kasuwan da yayi fice a aduniya tofa iyayen Mudda Sai suka dauki malama kamar wata silan bunkasan dan su kowa Sai ita ga rashin haifuwa amma bawanda ya damu Sai itace ma ta damu Tashiya tabi Mijin ta Yana America alokaci
Kwajin farko aka samu matsala a ajikin Muddakam amma bawai bazai iya haifuwa bane wani baiwan Kwan haifuwane dashi wanda yake da karfi sosai wanda acikin maza 100 da wuya asamu irin sa shi nashi Kwan Yana da karfi idan ba na wanda yayi daidai da nashin ba bazai iya haifuwa ba saboda Yana shika cikin mahaifan macce inde ma karfin su daya ba to narkewa yake atake ko 1second bazaiyi ba

Shine yasa zakuga wani yayi ta aure aure bai haifuba Sai ace baya haifuwa idan macece irinsa Sai ace juya ce rashin dacewa ne shiya turawa idan zasuyi aure Sai sun kwada amma ga muslmi bai hallta ba."

Abin yabigi Malama da mudda dan suna son haifuwa musammam Malama

Mudda yace "yanzu ba zamu haifu ba Kenan."?

Zaka haifu idan kayi dace da daidai kai amma ba da wannan matar ba,
Haka ita ma zata haifu Sai de amma bada Kai ba ita bazatayi wahalan samun daidai ita ba inde zaku Hakura da juna."

Ina daga malam har shi ba yanda zasuyi su hakura da juna
Haka suka dawo gida jiki a sanyayi

Mukaddam ya kasance mutum Mai harka da bokayi sosai kunsan manyan yan kasuwan nan da yan siyasa bakowa yakeda tsarkakaken zuciya ba afile suke mutane amma aboye halin su Sai su

Haka ita ma malam  aboye tana bin Malaman subbu abin har ya kazanta ita kam  gashi afili idan taga Mijin ta Yana wani abun yanzu zata dinga jawo aya tana fassarawa da take yawan sashi kunya yafara boye mata dan shima bazai iya dena bin malamai ba
Dan abone da yagada tun yana yaro uban sa ya koya basa bin bokaye da malamai

Malama duk da  halaye masu kyu da ta nuna afili ta samu dangin mijinta amma awai aikin malamanta
Shiyasa akace kayi aiki da abinda malami zai wa azantar amma idan kaga halin sa kar kafi
Bawan da zai ce malama tana da fuska biyu abune da hankalin mutum bazai iya dauka ba

Akawi wani tantirin boka tun na mahaifin Mukaddam muda ya yarda da boka *AUTA* bai taba bashi failure a aikin saba

Malama da taji bazata Haifu ba tasamu Aminu
Aminu amincecen Mudda ne shi yake guda nar masa komai

"Malama ance kina son ganina.?

"Aminu bawani boye boye wani temako nake so kamin."
"Malama bawani temakon da zaki nema inada ikon sa ban miki ba ."
"Aminu wane boka ko malami ne amincecen yallabai."

"malama AI yallabai baya bin malamai koda da yanayi yanzu yadena kin shawo kansa  keda ki keyiwa wasu ma wa azinnan balle Mijin ai yadena tun.....
"dakata Aminu kar ka maidani karaman yarinya mana,
Aminu nasan dukka motsin ku kaida uban Gidan ka katsaya kaji temakona kawai."

"to malama me temakon."

Kasa kasa malam tayi da murya tace "an tabbatar min da bazan haifu da  mudda ba
Kuma naje wajen bokana ya tabbatar Minda bazan haifuba amma duk ba wannan ne damuwar ba damuwar shine mudda yanada rabon haifuwa kuma wai kwana kusa amma boka yace min na samu amincecen malamin muda  ko boka sa zamu hada karfi da karfi da karfin awai aikin da zai min na mallaka Wanda Sai yanda nayi da mukaddam."

Aminu yace"wllh malama  AI koyanzu kingama  da Sir ban taba ganin macen da take juya mijinta cikin sauki ba irin ki Wllh da nazata kawai tsabar ilimin kine yake tafiyar da komai naki daidai da nusuwa Ashe de k....

Murmurshi malama tayi tace "karasa mana."

Shima murmushin yayi ya sunkuyar da kansa

"Idan da ilimin ma da temakon masu aiki da gagggawa na samu kan mijina da dangin sa dan da farko naga alama Sir bawani so yake minba Sai nayi wata guda bai kirani ko awaya ba Sai da aiki ya haukan sa bawanda yasan sirrina Sai Kamal
Sai Tabawa Sai Kai."

Tabawa me aikin tace wanda ita tafara koyawa malama komai kuma daga can rigasa ta dauko ta

Kamal dan gidan yayar malama ne yataro gidan mu yazama kamar yaron gida kuma shi malama ta dauka driver nata acewan ta shine muharraminta aboye kuma tayi haka ne dan yarike mata sirrin ta tunda bawanda yafi kusa dakai irin direba ka

Aminu da malama agaban boka Auta bayan malama ta siyi Auta da da manyan kudi da Mukaddam baya basa irinsu ya yarda da zai mata aiki duban farko yaga awai aure da mukaddam zaiyi kamar yanda nata malamin ya gaya mata
Da ganan yamata duk abinda yadace sukayi sallama

*Bayan shekaru 10*
Awanan lokacin malama tayi fice sosai wajen wa azi da sadaka da temako tayi suna Malama Hajara har kasashen ketare ansanta

Kamal ne yake jan malam a get na farko malama ta sauka dan hango wani buzu me gadi su da wani dan uwansa tana son buzun dan yana da abin dariya ko zata ji sanyi dan awajen wani bokanta take yagaya mata wani abu yana son faruwa da ita shine gaban ta yake ta faduwa
ta nufe su

"ah ah buzu dan fillo bak'i kayi ne."

"Malama ba baki na bane bakin najeriya ne yazo neman yariyar sa Yana kuka na gansa awaje shine nace yashiko na bashi abinci ga yaron sa."

Sai asanan idon ta ya sauka akan yarinyar da take ta faman gansaran abinci fari da kyan yarinyar bazai fadu lokaci guda ba budurwace zata Kai 15 ko 61

"bakon buzun da sauri yafito da pic na ya matso gaban ta yana nuna ma wata acikin hoton da yake alama family ne mutumin ne Sai wata da alama matar sace Sai wata budurwa da samari da Yara mata kanana 2 su 7 acikin
abin mamaki Sai taji shiden ba Yaren su buzun yakeyi ba shi shu awa yakeyi ita kuma dayake ta iya larabci tuda malama ce sai Sai sukayi magana babbar budurwa cikin pic din yanuna yace yarsa ce wani Doc a Nigerian yaje ya Aura sama da shekara 11 shine yafiyo neman ta dama su 5 ya haifa amma duk sun mutu a guguwan da ya afka musu har matar yara sa Sai yarinya daya ta rage masa yanuna wannan yarinyar kar ban pic din tayi tana sake kallon yarinyar da yanuna

mata tace "yasunata yace   *Ruwaiya*  wannan kanwar tata kuma *Karajina*
malama  tace meyasa Zaka aurar da yarka awanda baka San inda yake saune ba."
Cikin kuka yace yace" Yana yana Nigeria."

tayi mugun tausayawa mutumin da ganinsa dan kauye ne sosai wanda mutane kansu kamar ma tsoron su yake ji musamman
Yar tasa Sai wani zare ido take
Malama Tace "shike nan amma kazauna anan zamu nema maka ita amma yanzu garin nan ba karamin gari bane kar kufada wani hannun  malama akwai Nuna  tausayawa  godiya  bakon balaraben yamata tace daga wane gari kuke.?
Yace "mu shu awan jejin chadi ne".

Malama tacewa buzu to  ka kaishi part dinku ya huta da alamun gajiya."yace "
Ita kuma ta kama hannun yar budurar da banda wani hamanin wari ba abinda take dan datti kamar an tono ta ga gashi amma gashin ba kyan gani awani dankare da gani bai taba jin me taza ba
Suka shiga

Hajja tace " y'ata abin alfaharina anya tausayinki da kwshe kwashen ki  bazai sa wataran ki jawowa kanki wani masifan ba kidu ba yanda kika dauko wanda maki san asalinta suba kika ajiye kashi yanzu Mukaddam yace Yana mafarki da ita wayasani ma ko maiyace."

Murmurshi malama tayi cikin ladabi tace "Hajja Allah sai kiyaye

Hajja ta sake cewa "to yaushe zasu tafi ne."

Malama tace "Hajja ni abin ne yake bani tausayi   wai y'arsa yake nema Wanda wani daga nan Nigeria yaje har chat ya Aura ya taho da ita to bajima da auren ba sukuma inda suke aka musu wani guguwa me karfi ya afku sanadin hakan yarasa matar da yaransa 3 da wasu dayawa adangi shi shine suka tashi awajen dan dama guguwan ya addabesu dan yawan Saharan wajen  to bai sani ba ko ita yar taje neman sa bata sabuba shine yadauko photon ta yazo yana yawo nace awane gari suke yace Nigeria narasa kan bin ne."

Hajja tace"to kinjifa angaya musu Nigeria anguwa ne da zasu zo suna nuna photo ke kika daurawa kanki."

Shide Mukaddam yana jinsu dayake bame yawan  magana bane amma gaba daya hankalinsa Yana kan zancen yarasa meyake damunsa akan wannan yar araf din da ko yarenta bayaji

Abu gamar wasa Mudda yakasa zuwa wajen harko kinsa zuwa yanzu yasan son wannan yarinyar yake

Cikin dare malama tayi juyi sai ganin mudda azaune tayi yazuba uban ta gumi

Ta shi tayi
"alhaji meke damun kane kakasa gaya min amma ni dan so da damuwa da Kai nagane da muwan ka nace son yariyar nan Kake kace ah ah baka daukeni yanda na dauke kaba kuma ni yanzu amatsayin yar uwa nake awajen ka kacire batun komai duk abinda kake so nima inaso."

"Malama meyasa zuciya bata shawara Wllh zuciyata bemin adalci ba baki cancan ci kishiya ba daga ni har dangina muna samun nusuwa dake da baiwarki da ban San me zuciyata take nufi da son wannan yar kauyen ba....

Malama jin zuciyar ta tayi kamar zai fashi idan aka fasa zuciyar ta ba abinda zai hana aga hayaki ayanda yake aiki kasa daurewa tayi ta fad'a jikinsa tana kukan bakin ciki afili kuma wai kukan murna take

NACE UMMM

"nagode alhaji da soyayyar ka gareni muyi wa Allah godiya wata kila abinda muka jima muna nema tsawon shekaru 20 Allah zai bamu yanzu Insha Allah Karaji rabon muce."

Malama agaban boka Auta
"nagaya miki HAJIYA auren nen ba makawa to ke meye damuwan ki bade dukiya ba Al dukiyan Mai kwano ayanzu ikon kine."

"Auta nasani aure ba fashi bance ahana ba amma bana son yanda yake nuna son yarinyar ba ya iya biye sonta ko agaban waye yarinyar da inda Allah yabani haifuwa na ajiye irinta 5 amma Sai wani rawan kafa yake akanta iyayen sane ma suka ture basa so da kyar na shawo kabsu da kaina suka amince."

"to yakike son ayi yanzu".

"yawwa Auta inason amai data kamar wata tunku dangin Mijin suji ba abinda suka tsana irinta shima ya tsane ta sannan naga yarinyar kamar bulkuma ce inason ka sake kara mata wawan taka sannan bana son koda ma aikatan gidan suna janta dan kar takoyi Hausa da turanci da shine Yaren gidan tana zaman daki koyaushe nake so kaga hakan zai sa mulkinta ko da yaushe yana hannu na tunda ni kadai na iya larabci ."

"angama ko hauka kike so za asamata."

"ah ah bance hauka ba sabo da alhakin Sai yayi yawa."

"HAJIYA kina da tsoro."

"kai ko ba dole ba lashiran ma inaso nasamu Al shiyasa."

Dariya Auta yayi yace "hajiya duniya tamuce lahira banda mu."

*To masoya muje zuwa  ya karajina zata kasance idan ta aure Mudda m kwano*

*B Jattko*
[9/17, 11:11 AM] Batul Adam Jattako: AMFANIN  SOYAYYA*

*NA*

*BATUL ADAM  JATTKO*

Kainuwa asso🤝🏻

*8*

Da kyar Mattawa  baban Karajina ya yarda da auren bayan Sharuda da alkawarwura da Alhaji Dashiru ya masa na bazasu ci amanan sa yanda wancen yaci ba kuma ana daura wa da waye gari zasu tafi kasan chat din harda shi dan a dauko sauran dangin suga inda suke kuma za acigaba da nema masa y'arsa

Andaura aure
KHADIJA  KARAJINA da MUHAMMAD MUKADDAM cikin farin ciki

Ango ya angonce dan jiyayi amarya komai yayi anshirya mata wani dan karamin part a gefen na malama
Kamar yanda Alhaji Tashiru yayi alkawari haka ya shiyar tafiya chat  amma amota zasu tafi abuja Sai su tashi a jirgin da mallakin Mudda ne

Tafiyan ajalin Muda da Mattawa ne amota daya
Suna barin kaduna tayan su ta gaba ta fashe gigicewan da driver yayi shi yajanyo musu mugun hasari wanda kana gani kasan bawani mai rai ciki   dama su hudu ne acikin motan hatta motan Security da yake bayansu ya samu buguwa amma bai fadi ba  Innalilishi wannan family sunga rashi  Hajja ana kwantar mata kawan mijinta tafara tsinewa Karajina tana cewa annoba ce me farar kafa tafito ta tafi itako Kareji duk tafisu gigicewa ga bajin maganan su take ba ga tana gani aka shigo da gawan uban ta gida yarikice acikin dinbin mutane ta fadawa gawan  uban tana kuka sosai tana neman malama ta mata bayani  daker Hajja ta hakura tabar Karaji ta zauna amma tsana duk duniya ba wanda ta tsana har yanzu irin Kareji

Bayan wata 4 Allah yabawa Kareji ciki wanda har yanzu Hausa ba jinta take ba  Hajja ta danyi murna da cikin amma de kullum cewa take ita bata ga abin Farin ciki ba da wanda ba asan

asalin saba shikam Muda yayi murna sosai cewa yake Allah yasa ta haifu namiji nasamu magaji Habubakar sadik sunan sa malama afili tafi kowa murna

Zaune suke abanan boka Aura Kamal Aminu malama
Tace "Auta yanzu yarinyar nan haifuwa zata cigaba dayi ina zaune ko."

Auta ya fashe da dariya yace hajiya zata haifu amma daga wannan inaga ba kari dan zamuyi amfani da aljani Jumbar idan tafara nak'uda zaije ya zauna tana haifuwa kafin mahaifan yakoma zai lalata mahaifan  shikenan ba ita ba kara haifuwa kuma zamu sa mata ciwon ciki me tsanani ke kuma ki hada baki da doctor yace da matsala a mahaifan idan ba acire ma zata iya mutuwa kinga idan ancire shike nan."

Dariya malama tayi tace" yayi maganin Kuka na autan bokaye
Amma idan namiji ne ina son Adan nakasa shi yanda bazai iya rike dukiyar ba asa masa kurgunta ko makanta."
Boka yace "Angama

Haka Allah yasauki Kareji Inda tasamu yarta Mace mekamada ita sak amma kamar yanda boka yace haka akayi aka cire mahaifa da sunan mahaifan ba lfy

Zokuga rawan kafa awajen Mudda

Aminu da malama da Kamal
Malama tace" ai tunda akayi haifuwan bamu samu zama ba haifuwa yayi kyu mun samu Mace da boka yace zai naka sata na hana nace tunda macece ya barni da ita yabar min komai ba zan taba barin taji dadi ba."

Kamal yace" ai da bari kikayi ya nakasata dan macen ma ai zatayi ilimi to ma yanzu meye abinda namiji zaiyi Mace bazata iyaba ilimi ko mulki,?
kuma kin manta zata Yi aure mijinta kina ganin bazai nemi mulkammu ba muda aka tara dukiyan damu wani yafimu iko."

"Kamal Kennan bazan taba Bari tayi Boko ba
Miji kuma K'ani ka UMAR zan Aura mata Sai yanda mukayi dasu."

Kamal yace "hakan yayi ya sunan yarinyar ne da de ance Habubakar za asa Sai gashi ansamu mace."
Ita ma dariya tayi tace "sai susa saddik'a Al."

Itako Hajja ta dauki yariyar amma da Mudda ya tambaye ta sunan wa za asa mata
Cewa tayi kasamu malama kuyi shawara yanda tace shike nan
Aiko malama cewa tayi asa sunan yayar Karejina da suka zo nema  AISHATU RUWAIDA

Muda yana falon yana aki a laptop dinshi malama ta zo wajen sa ta zauna ya dago ya kalleta ya janye laptop din yana murmurshi yace" kinjini shiru ko sorry kina hakuri na sani."

"umm ai nasaba abinda Natashi dashi tun ayarinta ai yazama jikina,

Amma ni yanzu magana nazo muyi akan tilon yar mu Alhaji tunda y'ar nan ta fito duniya nake jin wani sonta shine nake son muyi shawara akan Kare lafiyar ta."

"Eh nima yanzu Wllh duk duniya ba wanda nake so kamar Ruwaida yanzu haka na maida duk malakin dukiyata yazama nata sabo da kin san mace bata cin gado ita daya ni kuma ayanda na wahala bana son ace yar da na mallaka kwaya daya an bata wani kaso aciki ba dan ina son Ruwaida duka takardun mallakan komai nawa ya koma sunan ta dan mutuwa baya sallama."

Wannan Abu ya dugunguza malama bata taba tsammanin Mudda zai zartar da wani shukunci ba tare da shawaran taba wai ya mallakawa yarsa komai sufa ai ita ma zata iya bugan kirji tace da ita aka tara dukiyar tunda bata san meye jin dadin zama da Miji ba kullum yana yawo zuciyar ta yafara wani irin zafi kanta ya fara sarawa Amma dan kada ya gane ta danne afili tace

"Masha Allah nima shawaran da zan baka kenan amma ina son kada kanunawa duniya kabata dan ni ason samu nama kada kanunawa duniya kana da y'a iya najikin mu ma mugob'e su da yad'a haifuwan nan."

A firgice ya kalleta yace "meye dalilin hakan ina shirin yin liyafa".?

Saboda hau da bakin mutane kasan bakin mutane guba ne sosai shine zaka ga yaran masu kudi irin ku dayawa ana samun batattatu aciki balle mu me kwaya daya tak ina son har girmanta muna tattalinta musata a islamiya ba Boko ba sannan koda tazama budurwa bazamu nuna yarmu bace saboda tasamu wanda yake sonta da gaskiya dan nasan mijin da ya aureta shine zai cigaba da juya dukiyar ta kaga bazamu so ta auri wanda ba son gaskiya yake Mata ba."

Mudda shiru yayi a nashi lissafin har ya lisafo manyan makarantu masu tsada da Ruwaida zatayi amma Shawaran malama abin dubawane tunda ancire mahaifan Karaji balle yasa ran samun wasu yaran yana son Ruwaida baya son baki ya kamata dan haka

yace "hakane magananki yanda
Ki kace shiza acigaba dashi dan haka na mallaka miki Ruwaida kece zaki koya mata duk wani tarbiya yanda yadace dan wannan uwar tata metasani."

Shan nono kadai yake hada Ruwaida da Karaji ba abarinta awajenta har aka yayeta malama ita da kanta take kula da Ruwaida Sai Tabawa ita Kareji Sai tayi sati bata ga Ruwaida ba

Karaji yan aikin gidan ma sunfita daraja agidan ba mezuwa yace matar gida ce ita de zata ci

zata sha amma haka take bata san komai na rayuwa ba  tunda take bata daba rike kudi a hannun ta ba koda yake kota rike mezata tsiya hatta sadakin ta Yana inda babata ya ajiye mata daga masu aikin har mutan gidan ba me kulata  Sai Harira Harira kanwar malama ce  ita take dan koya mata Hausa aboye har tafara ji

Bayan shekara 19

Sai da nayi wayo sosai
nagane Karejina matar gidan ce bansan itace  uwata ba Sai de ina mamakin yanda muke kama wata rana nake tambayan Harira ta gaya min daga nan nake zuwa gaisheta Sai de bawani fira sosai a wanan lokacin nasamu shiga A B U Zaria Qur an zalla nake karanta nayi sauka tun ina da shekara 15

Ko amakaranta ba asan ni y'ar Mai kwano bace zanji ana ta firan bashida da ko nadin gajin wa azin malama
Nide bani da kawa balle na tanka dan malama ta hanani shulda da kowa kullum ina cikin hijab har kasa da nikaf ba wanda yasan ni budurwace

Kakata Hajja balefi  tana nuna kulawa agareni umma tace de har yanzu bata so

Watarana nazo gida na tarar da get ancan za masu gadi bawanda nasa ba dasu bane

Fisari sosai nake ji dan de ina tsoron jeji ne ban tsaya ba hone nayi amma suka ki bude min daya sojan ne ya leko

yace "yakayi ne."
Tace "bangane ba bude min za ayi."
Yace"da izinin wa za abude miki."

Nace"bangane ba har Sai na nemi izini zan shiga."

Yace "haka  ka idan aiki yake."
Nace "to awajen wa zan nemi izinin."
"wajen wanda kikazo wajen sa kuma kicire wannan abinda kika rufe fuska dashi tukun.

Nikam abin dariya yabani   ga fisari ya dameni Sai nasaki dariya sosai

Abinka da soja kawai Sai yazuciya ya fara fada wani murya naji abayan sa Yana cewa "ya akayi Matawalle."

Wanda yake fadan ya Kwashe  abinda yafaru ya gaya masa ya daura dacewa haba me ake da aiki a Nigeria arasa inda za aturo mutum Sai inda za arena maka hankali nifa bazan iya service din nan agidan mutane ba gaskiya."

Dayan da yake bayan azuciye Ya bode kofan motan ina ganin fuskan sa dariyan da nake ya makale ganin irin kyansa da kuma kamar nasan irin fuskan amma banga ma tunani naba naji an wunsiloni waje tare da cire min shijab da nikaf alokacin daya amma me shima cak ya tsaya Yana cewa " *Kharajina* nima da sauri na kalleshi jin ya ambaci sunan  Umma na amma na dauka yazata  itace tunda muna kama

Dayan naji
yace" haba *MALL* wane irin Kharajina kuma kana wannan siririya kuma tafi Kharajji fari dan kama suke."
  wanda aka kira MALL yayi shiru yace koda yake ance da irin wannan kaman aduniya
Afili kuma yace "ke kiyi litdown  ki nada hankali soja kikeyiwa dariya."

Najuyo ina kallon sa wani irin tsawa da bansan irin sa ba yadoka min wanda yayi sanadiyan kufcewan fisarin da nake dannewa bansan sanda na zube guiwowuna biyu a kasa na daga hannuna ba abinda ban taba inshiba yinshi ba ko a primary school kukane ya kufcemin Bajimawa Sai ga Dan zomo wani yaron gidan mu yazo shiga aiko da sauri yayi parking  yafi Yana cewa "yasalam!  Madam ya akayi ne  yamusu bayani suka ce Natasha shi wanda aka kira da Mall har yanzu kallo yake bina da shi yace "kobe ma kiyiwa soja dariya."

Fadawa tayi cikin malama tana kuka ta gaya mata aiko malama ranta yab'aci sosai ta kama fad'a takira Murtala anan yake gaya mata dan gidan gomna  Matawale  aka kawo services shine tamusu abinda bai kamata ba amma ayi hakuri basu santa bane

Malama tace " Ruwa kiyi hakuri dan gidan gomna ne zaiyi service shine baban sa yace yayi anan YA yarda da yawan security din gidan nan
Kiyi hakuri kidena shiga harkansu kinji. "
Ruwa tace" shikenan."

"Malama Bari naje na gaida Umma."

Malama bata son taji Ruwaida ta cewa Karaji Umma

"ina Hajja nashiga bangarenta ance tayi tafiya?"
"Eh taje Maiduguri gaisuwar kawarta tarasu."
nace "Allah yaji kanta.
Afita

Akan gado na samu Umma sai rawan sanyi take ga AC a kunne hakoranta sai hadewa yake da sauri na hau gagon
"Umma meyake da munki ki.?
Nadago da ita aiko atake ta kwaro wani amai Sai yunkuri take da guduna fita part din malama tare muka shigo da ita ta daga Umma sosai tayi wani fari ta rame cire mata rigan jikinta malama

tayi tana cemin hada min ruwan dimu a wanketa a kaita asbit....
Maganan ne ya makalewa malama ganin yanda cikin Umma yagirma."

Tajima tana jinyan amma dayake tasan ba mahaifa ajikinta yasa bata damu ba amma yanzu GA ciki yagirma amma tace Al wata kila wani jinyan ne acikin ta ba ciki bane

"Malama zan biku hospital din."
"Ah ah Ruwa zauna ki huta daga zuwanki."

Malama da doctor

Wllh Hajiya patient dinki ciki gareta harna tsawon wata 6 amma me dalilinki na kin yarda."

"shike nan doc nagode dama ganin tajima bata haifuba ne na kasa yarda akwai goron albishi na musamman."

Jiki na rawa malama takoma gefi ta kira tsohon doc nasu Tanimu

"ranki yadade uwar dakina."

"Tanimu Haka zaka min kace kacire mahaifa tsawon shekara 19 amma yanzu ciki yafito ajikinta."

Baki na rawa Tanimu yace "HAJIYA ganin na auna banga komai ba kuma ganin ke alokacin kindamu acire ne yasa nace miki nacire dan ki kwantar da hankalinki dan nasan ciwon bai kai acire mahaifa ba dan de kin tsorata ne.....

Al bata karasa jiba ta kashe takoma ta kama Karejina take ta shan wuya suka fito zuwa inda Kamal yayi parking ya kaisu ta na kwantar da Umma adaki takira Kamal da Aminu suka fita Wajen Auta
Auta yace "doc ne ya b'ata aiki amma yanzu ciki yashiga wata na 7 yafi Karfin alalata shi saide idan zamu Bari ta haifu sai asan nayi."

"Wllh Auta bazan Bari ta haifuba saboda yanzu haka Wllh Alhaji komai nasa Ruwaida shawaran komai ita ce me bashi ga yarinyar shegeya wai har wasu mata ta dauko ana koyawa Ummanta yanda ake kwalliya da turanci yanzu har ta fara wayewa balle ace tasake haifuwa ina Wllh bazai ma yuwu ba kawai kane mo mana mafita kawai."

Boka yace" ansan da cikin nata ne."?
"Ah ah iya mune muka sani Sai ita inaga tasani Al."

Dariya boka yayi yace "shikenan ma kije ki tsare ta adaki kada kowa yasan tana da ciki in zan tura aljanu su cusawa ita Ruwaida cutan masu ciki ta dinga amai da zaben abinci idan lokaci

haihuwan yayi ki tambatar ita Ruwaida tana wajenta ta haifu a daki mukuma zamuyi aikin mu awaje mu haukata uwar San nan mu ballowa Ruwaida jini da ciwon ciki kamar ita ta haifu amma hakan bazai yuwu ba Sai kin hada da Tabawa da doctor  kin tsaye su

Ita kuma uwar a haukan zata dinga sinewa yar tace ta haifi cikin shege kinga ba yanda za ayi abawa mijinki abinda  aka haifa sai Ruwaida idan yazo zamu sa masa tsanan Ruwaida yakoreta su shika duniya ita da dan kinga dama bawani saninta akayi ba dukiya yazama naki,

Amma idan watan haifuwan ya kama ki dauke wannan surukar taki Hajja
ki tabbatar Mudda baya kasan."
"to Auta hakan yayi amma de kawai ba yanda zanyi ne bana son haukata ta saboda akwai zunubi sallahn ta azumin duk akaina yake."

Auta yace "shikenan zamu sa tawarke bayan ta shiga duniya."

"yawwa auta ba inda ta sani kodaga nan kaduna aka kaita wani wajen bazata iya kawo kanta gida ba."

Handcacheik a Hannun ta tana da tsartar yawu aciki tuda ta shigo parlour Hajja take karantan yanayinta

"Ke dan Allah tashi kin dameni da tsarte tsarte kamar wata me ciki."

"Allah hajjaju zuciyata tana yawan tashi gashi komai naci Sai na amayar kuma komai na taba Sai naji kamar an shafa danyen kwai kinsan ni ba son warin sa nake ba."

Hajja tace
"kode kina da tsusan ciki kije kiga likita kawai."

"to."

Malama adakin Umma Kareji tace "Karaji ya jikin naji."

tace "da sauki yanzu meyafi damunki."
Tace "zazabi ciwon Kai amai shikenan."
"Ok yabaki magani zaki dena sai de nayi mamakin da kika boyemin abin farin cikin nan kina dauke da ciki har na tsawon watanni 7 baki gaya min ba."?

Saurin rife fuskanta tayi alaman kunya

Murmurshi malama tayi tace "Khadija kin biyamu  Allah yaraba lfy amma ina neman wani alfarma awajenki."

Dasauri Kharajana tace "nikuma ki fadi kome ki keso zan miki ke daya kike sona kece gatana ke kika san maraicina ni bani da kowa saike abinda kike so nima ina so."
"Yawwa yar kanwata ina son mubawa Mukaddam  mamaki wato muyi suprise dinsa kada yasan kina da ciki har Sai kin haifu zai fi nuna murna sa zai kara sonki har ita Hajja nasan Sai takara sonki idan suka ga d'a daga sama kimarki zai karu hakan ba
Zai yuwuba harsai kinboye cikin nan yanda hatta ma aikatan gidan nan karsu san kina da ciki idan suka sani zasu yad'a kowa yasani."

Washe baki Umma tayi dan tana son surukar ta da mijinta su sota itade tasan ko a kauyeso ba haka mata da miji suke zaune ba idan taga Mukaddam a part dinta to tsananin bukata ya kawoshi yana gamawa zai juya baya zama da ita yayi fira haka agidan ma wajen malama kawai take jin sanyi

"to dama nasan bawani fitowa kike ba kina rufe kofanki sosai shi kuma Mukaddam gobe zan tafi kasan da yake dan karyayi mana zuwan bazato har da Hajja zan tafi kawai ranan da kika haifu Sai muji Sai muzo atare,
Itan kika ji nakuda ki sa akira Tabawa da Ruwaida kadai sun Isa sai doctor  Habib amma ita kanta Ruwa Sai kinzo haihuwa ki gaya mata gudun kar ta gayawa babanta kuma kada ki kuskura ki haifu ba tare da Ruwaida awajen ba kinsan yanzu duniya ba yarda shiyasa bana son kowa yasan kina nakuda inba doc Habib da Tabawa da Ruwaida ba."

Malama a bedroom din Hajja Sai Ruwaida
Malama tace
"Hajja Wllh ina son muje China tare naji labarin wani shahareren doctor akan cikon kafanki."

Washe baki Hajja tayi
Tace" kamar kinsan haka nan ma yawon nake so kinsan idan nadanyi yawon nan Sai kiga naware sosai yau she zamu tafi?. "

"gobe insha Allah Mudda ma yana can ai."

Ruwaida tace "malama nima zanje Allah bani da Ify."?

"ah ah Ruwa kiyi zaman ki kinga kina cikin karatu nikuma idan naje bazan zo dawuri ba zamu huta kamar wata3 haka."

"to Al saura wata 1 da sati 3 mu fara exam muna gamawa zan biki."
"OK Sai mungan ki."

"Kamal ka tabbatar anshafa danyen Kwan nan a jikin motan ko dan kasan dole ta raka mu idan taje jikin motan taji k'arnin kwai dole tayi amai daga nan ranan da komai ya faru idan ance ta haifu kaga Hajja bazatayi mamaki ba"

Washe gari
Hajja kan har tashiga mota dan sunso su makara

Malama da Ruwaida atare suka fito Sai faman lallashin Ruwaida take har suka  karaso wajen motan Ruwaida ita ta bude wa Hajja ta shiga
Wani irin yunkuri Ruwaida tayi da karfi wani amai yazo mata kamar zata amayo da hanjin cikin ta da sauri malama ta fito ta dafata tana jera mata sannu

Ita ma Hajja fitowa tayi tana "ikon Allah ni Fatima  Al amarin yarinyar nan da mamaki yarinya kamar me shigan ciki gai....

Daure fuska malama tayi "haba Hajja wannan wane irin fatane ni nayar da da tarbiyar da na bawa y'ata typod ne kawai kinsan wancen karan ma haka tayi Tabawa kamata kushiga ciki ki Kira doctor  Habib yadubata."

Suka shige suma driver  yaja dan sunkusa magara

*Tofa masoya yanzu muka shiga labarin Ruwaidatu  fa me ra ayinku akai*

*B JATTKO*
[9/17, 11:12 AM] Batul Adam Jattako: AMFANIN SOYAYYA*

*NA*

*BATUL ADAM  JATTKO*

kainuwa asso

*10......*

Ruwaida tana ganin ya seta ta tayi saurin zubewa a kasa ta yiwa Abdallah runfa dan haka ta samanta bullet  din yawuce
Jikake tass bullet din yafasa glass din mota
Dukka kowa yayi cirku cirku awajen

zai sake setawa da sauri malama ta shiga tsakani tana kuka tana cewa "Alhaji kadinga cewa innalillashi  baka San cewa idan kayi kissa  ko awayen Allah kafi Ruwaida lefi ba."

Ruwaida tashi tayi ta karasa inda malama take  ta fad'a jikinta tasaki kuka shima jaririn Sai kukan yake

Malama tasa hannu ta karbi jaririn ita ma kukan take a zuciyar ta kuwa cewa take bata taba ganin kama irin na jaririn nan da Mukaddam ba  dan tanada pic na Mudda Yana jariri kamar shi take gani take wani tsanan dan yakamata amma afili  runguman shi tayi idon ta Yana fitar da hawayen bakin ciki
Ruwaida ce tafara magana cikin kuka

"Malama kingani ko da Abba yake kama d'an sane Wllh ummata ce ta haifu nasan ke kadaice zaki yarda Dani nasan zaki fashimtar da Abba."

Itama tace Ruwaida bani da bakin da zan fashim tar dashi akan abinda idon sune fa Yagani jinin haifuwa Yana fita a jikin ki sannan Ummar ki da bakinta ta fada Ruwaida kine mi tuba awayen uban ki kifadi wanda yamiki wannan aikin dan nasan irin tarbiyan da nabaki bazaki taba aikata zina ba waya baki fyade.?

Ruwaida daura hannuta tayi akai
tace "nashi ga ukku  malama ban san me zance ba gashi ba lokacin wahayi bane balle Allah yasauko min dashi amma nasan yana ji kuma Yana gani tunda ke baki yarda dani ba nasan ko Qur ani naci ba me yarda dani said....

Hajja ceta katse ni dacewa "Malama mekike jira da tsitaciyar magen nanne da bazaki bari ta tafi ba ko kina so narasa d'ana da ya rage min aduniya."

Malama gaban Hajja ta zube tana kuka "Hajja ke kadai zaki temakeni wajen shayo kan Mudda ya yarda yabar min yarinyar nan saboda lefin da tayi bai kai hukuncin da ya yanke na koranta ba ina yake son Ruwaida taje......

Da sauri Hajja ta katseta da cewa "malama kar ma ki fara tun barko alfarman kine auren uwar ta tsintaciyar mage gashi yanzu me ta k'ara mana inba tozarci da asara ba kituna narasa mijina a dalilin su bazan rasa d'ana ba tunda yace bazai Iya cigaba da kallon taba taje ko ina ma."

Malama tace
"Hajja kituna Allah yac......

Mudda yayi saurin cewa "malama ayau wa azin ki ba zata karbu ba awajena  Wllh idan ruwaida ta sake second 10 a gidana  sai na kasheta."

Malama tace "to kamin alfarma daya ina son narike jaririn nan kasan shi bashida lefi m.....

Kafin ta karasa Mudda ya mata wani irin tsawa wanda duk wanda suke wajen Sai da suka tsorata

Hajja ce  kar bi jaririn a hannu malama tace "ungo k'azan tanki fice mana agidan tashiga tura

Ruwaida har ta fitar get  tacewa sojojin su fitar ta

Ko takallmi babu haka nafito agidan ubana Mukaddam me kwano da ake yiwa lak'ani da *YARO DA KUDI*
Haka na dinga tafiya ga katangan gidan mu kewaye shima aikine dan gwangwani guda ne gidan mu

Ina shan kwana na ga motan Mama Harira  glass din tarage ta leko tace"shigo Ruwaida na zagaya na shiga

Tayi gyaran murya tace " da farko de zan fara da baki hakuri kan afinda yafaru ina dasa hannu ciki  Ruwaida malama kamar yanda kika sani uwa daya uba daya muke da ita amma gaskiya na tsani malama saboda mugayen halayenta ba yanda na iya ne nake mata biyayya amma ina jiran ta gama daukan nauyin karatun yaran nawa su tsaya da kafafunsu da ganan da kaina zan fito na tona asirin  duk abinda take yin wanda ko mahaifan mu basu sani ba

Daga nan ta kwashe duk tarishi gidan mu da labarin da na bada ta gayamin

Mama Harira na gode yanzu kina da inda zaki kaini saboda wannan yaron ki temake mu".

"zan so haka Ruwaida amma ina tsoron malama kin sa mutum me bin bokaye ba afiye boye masa Abu ba amma temako daya da namiki ta bude cover motan ta ta dauko wani handbag ta meka min
Tace " wannan kudine da zaki dan Kashe aciki Sai pic na asalin UMMA ki da family ta da na dauko a dakin UMMA taki tun dazu nake nan dan nabaki ki nemi yayar Umma ki su kadai suka rage miki nasan zasu sabo miki mafita ga number na idan kina mukatan wani abu  ki k'irani tana gama fadan haka ta mekamin Key din  ta fita a motan kitafi da motan amma kar ki tsaya akusa  kuma idan kina bukatan meman Umman ki ki nemi Aminu   amma kar sunana yafito fato."

"insha Allah Mama Harira sunanki bazai fito ba nagode

Na sakalawa jaririn belt naja motan tafiya nake gani kifin cikin rijiya ba inda nasani ba inda muguwar malama ta barni nake zuwa ga dangin Abba amma ba gidan Wanda nasani kawai nabi kwalta har na wuce Zaria Sai da nayi tafiya sosai shima jaririn baccin sa yake Sai da taje Kano na kuzu cikin gari haka na dinga zagawa anguwa anguwa  na rasa yanda zanyi nayi parking akofar wani gida balefi gidan da girman sa kuma anguwan ma balefi    wani tagani Yana tafiya da sauri ta fito tace "Baba dan Allah temako nake son kamin."

Babban mutum ne yace "Allah yasa zan iya.""

Dan Allah gidan haya nake nema."

Kallo na yayi sama da kasa yace kina nufin awanan zamani haka kawai ake daukan gida abawa mutum haya batare da ansan inda kika fito ba koda yake kinji anacewa Kano garin b'aki ko to Bari nagaya miki bazaki samu gidan haya ba har se kinbi ta hannun me anguwa hima sai ya bincika sosai kafin yasa anemo miki."

"inane gidan me anguwan."

"Yana bayan layin nan idan kika zagaya kiyi tambaya."

Komawa mota nayi na dauki Abdallah na kulle motan na zagaya baya
tambayan da megari ya fara min ina jagora na wanda yasan gari aka yarda dashi wanda ko wani abun nayi shi za anema ya nemoni San nan ni yar ina ce

"Nace bani da jagora kuma ni yar kaduna ce cikin shege nayi iyayena suka koreni."

Me anguwa yace Kai Kai basu kwauta ba ai yanzu ciki yazama ruwan dare amma agani na kibari na hadaki da mutane aje aroki iyayen naki dan zaman kyakkyawan Macce irinki a bariki ba karamin hassari babe."

Ya dauko min wani nasiha da bana gane meyake cewa haushi yabani dan haka tun da sauran mutumcinsa a idona na meke nace Bari na dauko kayana a can

Jin ginuwa nayi ajikin motan na zauna ina kuka yanzu idan me anguwa ya kaini Abba ya hakura haka zan zauna da azzaluman malama tana bunnemu da ranmu nida dan kanina rungume Abdallah nayi ina kuka nake cewa "Wllh bazan kaika ba Abdallah zan Bari sai ka girma mu dauki fansan abin da malama ta mana."
Hone da suke min ne ya dawo dani haiya cina na dado Kai wasu kyawawan yan mata na gani da gani kofar shigan su na tare dayan ce ta Karaso baki na rawa take tambaya na Ify me ya samoki kike kuka".?

Naci gaba da kukana dayan ma fitowa tayi ganin yanda suka rude
nace
" bakomai."

"To wannan motan ki ne dan matsar dashi mushiga da namu gida kinga garin da hadiri".

Key din na mekawa dayan."

Ta karba dayan tadan jani muka koma gefe ita daya ita tashiga da duka motacin har nawa tace " kinga mushiga ciki da alaman agajiye kike ga yaro yana kuka inji na bisu nashiga a parlour muka zauna

Meyawan fara an tace "ni sunana Ayya sai yarinyata ta shafo kan wata yarinya da bazata fi

shekara daya ba aduniya  tace ita kuma Barrat  Sai  yar uwata Hamrah nan gidan mune."

Nace "OK."

Hamah tace "kibashi nono mana yana kuka kuma gashi jariri ko cibiyar bai fadi ba ke ko me ya fito da ke da wannan jaririn da alama haifuwan Yau ne ko jiya"

Da sauri Ayya ta ajiye Barrat tayi kanmu tace " haba Ham ban gane ko cibiya bai fadi ba muganshi."
ta kabi Abdallah  a hannun Hamrah nide binsu kawai nake da kallo

Ayya da dafe kafada na tace "haba Sis nasan de ba lafiya ba fita da jaririn yaro haka dan Allah ki fada mana kome da gani gina cikin damuwa amma kafin nan ki bashi nono tukun."

cikin kuka nace "bani da nonon da zan bashi dan kuwa ba ni na haifeshi kaddara ce ta hau kan mu nida shi."

Ayya tace duk kaddaran ki baki taka Rabin namu ba sai....

Da sauri Ruwaida nace "duk duniya ba me irin *(KADDARA TAH HAUWA*
*A JIDDA)*

itama da sauri Hamrah ta katseta "karki fara tamu kaddaran da ban yake da nakowa."

Murmushi nayi nace "zanso jin naku Kaddaran inde yafi nawa."

Ayya ce tafara bawa Ruwaida labarinta sai Hamra
Cak Ruwaida tameke  gaskiya ne akai ban bance Naku da nawa amma ta wani bangare nawa yafi zafi kawai ni sauki na ba aketa min haddi ba ina tare da budurcina na
Kuma a gani na Ayya naki shine Kaddara amma naki *Hamrah* gan gancine da wauta

Da ganan ita ma ta kwashe nata tafada musu

juyowa tayi tabude baki zata gaisheshi sai dai dai lokacin wayan da yake gefen sa Yayi ringing komawa tayi ta zauna shima ya daga wayan yana cewa "Eh da yake tafiyar mota nayi shine na tsaya a kaduna gaida Ummata zan duba in sha Allah ok sai auren Mujja thanks.
ya kashe wayan
Ruwaida ko cika tayi fam ashe ba dan ita yazoba
awani gunya tashi ma
Itama Umma dan tak'ara  kular da Ruwaida dan ance mata Ruwaida bata san yasaki Halima ba tace "ko deda surukar tawa kake ne."
shiru Mall yayi kamar zaice wacce surukar sai kuma ya harbor jirgin Umma yayi murmushi yace "ah ah Umma ba ita bace kinsan nace miki tana fushi dani akan sai nazo da ita."
Umma tace ai da kazo da ita kaga bata taba zuwa ba dole tayi fushi."
"Umma nafa fada miki bata da lafiya."
Umma tace" hakane Allah de yaraba lafiya."
shiru yayi kaman mejin kunya
itako Ruwaida sai da suka gama maganan su ta juyo ba yabo ba fallasa tace "Yamall  ina kwana ya hanya.? duk tajera lokaci guda duk abin mutum bazai ce ga yanda fuskanta yake ba shima d'agowa yayi ya kalleta ya sauke kallon akan wayan sa yace "kina lafiya.?
ata k'ai ce
bata sake cewa komai ba  sai Umma ce tace "Hajja ta fito parlour ne .?
Ruwaida tace "eh
Umma ta mek'e tace" bari naje na gaida hajja.
Mall yace"ok .
tafita
Ruwaida ma mek'ewa tayi zata fita har tayi taku  3 ta tuno batun izinin amfani da waya bata juyo ba ahankali tace "inason zan fara amfani da waya."
Mall wani dadi yaji dan da yaga wayan a hannunta yazaci mata  fara amfanin ne
Jin yayi shiru yasa ta juyo saurin dauke kansa yayi kamar ba ita yake kallo ba
tazaci bai ji bane yasa ta mai daita
yana cigaba da danna wayan sa cikin basarwa yace "neman izine kike ko umarni.
Ruwaida tayi mugun kulewa da yanda yake mata magana kamar wata kashi
cikin k'uluwa tace "dukka biyu.
shima cikin i sa yace "ok ba da izinina ba kuma ban yarda ba "

kallon sata tsaya yi kamar zatayi magana kuma tama rasa me zatace zata juya ya dago kai yana mata wani  kallo ta dauke idonta
Murmushi yayi yace "kici gaba da kallonki halalinyan kine fa idan kina bukata kar ki cutar da gangan jikin ki dan akwai shisabi a tsakanin ku idan kin cutar dashi
Ruwaida tace "banga abin son ba kuma ban ga me hanani fara amfani da waya ba wllh."

hannu kawai ya d'aga mata alaman ya isa
tafita a fusace part din mlm ta shiga Dan tasan ita kadai ce zata sanyaya mata zuciya da kalamai masu gamsarwa
shiko mall ya zauna yana tuna randa Ruwaida zata sake shiga hannunsa yayi murmushi shide aduniya yasan bawani abu da zai so kamar Ruwaida ahankali ya furta lalle kincika INDON MATA.."
Umma tace "Allah Sama ilu.
da sauri ya bude idon sa dan bai san ta shigo ba murmushi yayi yace " sosai Umma kubani ita dawuri ko na taro gidan nan."
"haba kar ka badani mana."
sosa k'eyarsa yayi yace Umma Aisha cefa
bai de karasa ba."

Hajja sai bayan Mall yatafi taji labarin zuwansa tazo tayiwa Umma tatas har Ruwaida bata bari ba acewar ta meyasa bata kirata ba ita da take neman sa ta rama abinda yayi mata munafuka wato kina son mijin ki ko

Ruwa taga gata awajen Abban ta dan tafiya ya kamashi yatafi ba dan yasoba bayan yacika mata account  fal da kudi amma
shirye shirye biki ya kan kama dan har anfara gudanar da biki tun Thursday Ruwaida da Ayya suka sauka Ruwaida ansha fama da hajja dak'er da alk'awarin lalle ba ita ba Ismail kuma ana gama biki kafin ma su Unma suzo ita zata zo

Ummm to bari muga ko malam ILU zai yar da yasaki wannan dama

*ADAMAWA*

*HAMRAH* me kwana biyu yakoma sati biyu dan ita ma yau din  take shirin zuwa dan tana tafiya da kwana daya tafiya yasamu Sahal yazo sukayi sallama
Hajiya Hamrah wanda yanzu ta koma Auntyn family sarkin k'ira dan komai za ayi sai da shawaran ta yanzu haka ranan aure za a yanke agidan Hamra ceta tasa rana ta tambayi yaran kalan kayan d'akin da suke so da taga bawani sanin kan kayan da ake yayi sukayi ba kawai ta cewa Sahal ya saya musu irin nasu Kharajina
su baba Hamza tuni suka sa Baban hamrah ya taro gidan suna family yanzu kam son Kabiru kuruma ake sosai

Hamrah an mata rakiya  har mota kowa sai da yafito har moton yafita agidan ta ga kamar

zauren k'ira hayaki yana fitowa ta juya ta kalli Binta da Rabiya da zata wuce dasu Kano har sai angama biki su dawo tace k'ira har yanzu agidan nan wayake mana k'ira Binta tace " Ya Nura. saukowa hamrah tayi zata shiga zauren amma zafi ya hanata shiya a koma ta tsaya "Yanura da sauri Nura yajuyo fuskan baki k'irin ga toka da gawayi da gumi yayi masa kace kaca ba wanda zai ce shine *Alhaji Nuraddin Hamza sank'ira*
cikin murmushi Hamrah tace "sannu Yanuri gaskiya k'ira akwai wahala dole kace kai baza ka dauwama a sana an k'ira ba amma gado ba karan bani bane k'ira ba sana an rago bane kuma sai wanda ya gada dariya tayi tace wayyo har na tuno min da CABALLIYA a gidan mu gidan dadi kullum sai tamin wannan wak'an
*wasan wuta wasan wuta da ciwo yake ne hamratu k'ira ta gada*
kasan fa sana an k'ira sai magajin sa saboda abune da rago bazai iyaba haka bakware ya gaji shiga ruwa idan ka bashi k'ira bai isa ba shiyasa nake alfahari da sana ar gadona YaNura Allah ya temaka tajuya zata tafi ahankali ya mek'e nadama afuskan sa ba zai misaltu ba yace "Hamrah kiyafemin Dan girman Allah ."
"YaNura na jima da yafe maka meyasa kullum ka ganni sai ka nemi yafiya ne ? bayan yawuce na yafe nima Allah ya yafemin kurena."

"Hamrah na cutar dake dayawa amma hamrah idan da gaskene kin yafe min ki bani documents dina wllh akwai wani abokina zai nema min aiki takaddun kawai ake jira

."shiru Hamrah tayi
shiyasa tun a lokacin tace a ajiye kar akona Ruwaida da zafin zuciya ta kona su bata soba tasan irin wannan ranan zai zo dan koya naka yake nakane
"yaNura sai de kayi hakuri nagaya maka ankona su wllh amma in sha Allah zanyiwa Aunty Ayya magana aiki bazai gagara ba ko a companyn ta kafin nan ka tambayi Habibullah na bashi sako ya baka inaga mantawa yayi....
jitayi abayanta ance "ba mantawa yayi ba nina hana.
atare suka juyo duk da sungane muryar me maganan
Hamrah tace Wassilim meyasa hake haka kudina ko naka."

Wassileem da yake jin kansa ayanzu kamar shine gaba da Hamrah kudi ya zauna masa kuma gashi mijin *AMMA SHIDDAS BARNO*
aboki ga
*AKKARAM SHID*
yayi gogaiyya da manya yana ma kanyi dan idan aka irga masu kudin adamawa zai iya zuwa na goma ga temako  amma banda yan gidan su da yatashi da mugun haushinsu yanzu haka ban da sun kawo masa iyayensa ba abinda zai kawoshi kuma bayajin zai yafe

Hamrah tace "yanura taromin  account number  din ka tajuya shima Wassilm tsaki yayi yashige cikin gida tasan kafin ya huce sai tasha fama zuciya kamar shiya gaji kurmantan
*Kano*
shirin biki ya kan kama dolen sa yana dan shiga safgan bikin saboda abokin sa Mujjashid wanda zai aure Nafisa kanwar sa wamda suke daki daya da Sahal

ayau ne Tuesday za ayi match ball na bikin an sha fama da Mall akan bazai yi ba musamman da sunansa ya fito a Team amarya kamar ance yasake kallon takardar aiko caraf yaci karo da sunan ruwaida a Team na ango kan uba matar sada buga kwallo agaban dinbin jama a sai de idan fasa auren za ayi inde dole sai anyi March amma yasan bazai samu goyon baya awajen Ummi ba dan tana da son bidia Amma ceta fado masa dasauri ya jefawa matawalle rigan wasan da aka basa me sunan amarya gaba da baya nafi ajiki yafita sahal yace "ai dama nace muku shigen ba zai yiba shida yake ta fadan mujja ya zubar mana kima yaje yana wani soyayyya da yara".
dariya matawalle yayi yace "koni sanda nake soyayyya da Kharajina har nabar Kano bazai min magana ba sai gashi shima ashe yarinyar yajima yana nema sa arsu ce."
duk dariya sukayi sahal yace" sai ma kunga wahalan da yake sha tsohuwa ta hanashi matar sa." daga nan ya kwashe abinda yafaru ya gaya musu dariya sukayi tayi
Matawalle yace "randa yafara sa ruwaida a idon sa ya gigice nace masa ai itama yarinya ce batafi Kharaj ba haka yace tafi Shatima ma ".
Sahal yace "bawani ai shekara guda kharajina tabawa Ruwaida."

Umma ta Kalli Mall tace "to yanzu Samaila ya kake son namaka kabari kawai nasan ma Ruwaida ba zata ce zatayi wani Ball koda ba aure akanta."
nasani ita ustaziya ce amma Umma kisani idan irin wannan bikin ya taso wllh dayawa ajiye ustazancin akeyi kisamo min mafita shikenan zan hanata."

Ruwaida Umma ta hanata amma batace Mall ne yahana ba shima Mall bai zo wajen ba dan ya tabbatar bata jeba

Amma de anyi wasa me k'ayatarwa a inda Amarya Farida ta ciye angonta SadeeQ ita ma Nafi ita ta ciye ango Mujjashid da mutanen bayan sa
Ita kuma kharajina Affan ya lashe Affan dan gatan mommyn sa harda ita awasan ba kunya ta zage tanayi wanda basu san ta bama yau ga alk'arin AK'alai afilin wasa auren d'an lele

haka ran kamu Friday akayi kamu Mall de bai jeba amma yacika fam da yanda aka dinga posting hotuna a media yawanci da ruwaida aciki dan sunyi kyau ita da Ayya da Hamrah har kaman zasufi amaren haka aka dinka tsokanan ruwaida kamun harda ke dama ba amiki ba status ko yau ranan sane duk da ransa bai so yada hotonan ta ba amma baya gajiya da kallon su kusan dare yaraba dawaya ahannu gani yake duk duniya ba wacce tafi Ruwaida

Shagalin sai yau ake yinta yau general
Paty
Matar da aka dauko takanas dan kwalliyar amare da k'irajen biki haka kawai taji tana son Ruwaida da Ayya da Hamrah dan haka makeup din su daban ayanda ta tsara musu kwalliyar dole su dauki hankalin jama a Ruwaida ta Kalli kanta yanda kayan ya kamata sosai ta kalli Abida tace "aunty abid anya zan iya fita haha gaskiya kayan sun kamaki sosai wai baki bada measurements din riganki bane. "
Hamrah tace "wllh aunty dai dai ni akayi kuma tsayis dinmu daya baki ga ta kara cika ta k'irji

wllh Boobs dinta da Hips sun karu Zahariya tace "eh wllh sis me sirrin ne.? Abida tace amma gaskiya ba zaki canza ankon nan ba kiyi hakuri kawai ai bikine.
su ukku suka fito dan yawan ci an wuce suna fitowa kowa sai Masha Allah yake cewa iya wanda ba zasu je bane a gidan Ruwaida ce take ta dube duben wanda zai kai su dan wannan adon bata driver bane gwara su nemi me tuk'asu da k'er suka samu wani abokin lawan ya kai su har anfara gudanar da dinner hamrah ce afarko Ayya na binta sai Ruwaida da gabanta yake ta faduwa abaya dan taran abokan Affan suna wajen karsuyi abinda zai taba mutumcinta dan tasan yan tabara ne dukka sangartattu irinsa ne
duk angwayen kowa kusa da tasa amaryar Mall da kansa asunkuye yake acen gefi wani irin ihu yaji Hall din ya dauka
*kala abasu kala abasu kala* ko sautin kidan ba aji saboda ihon mutane juyowa yayi dai dai san da suka karasa tsakiyar filin wani irin zabura yayi ya mek'e

*saboda yanda labarin ya jima ne na dan kara yawan pages din in sha Allah a page 28 zamu tsaya kuyi min abuwa*
[9/17, 11:25 AM] Batul Adam Jattako: AMFANIN SOYAYYA*
( aure )

*NA*

*BATUL ADAM JATTKO*

*26*

Ruwaida ji tayi Mommyn Affan ta rungumota nan mutane suka shiga zuba mata ruwan kari harda abokan Affan
Hamrah Sahal yayi saurin taranta shima Grema taran tasa yayi suka zauna ita ko Ruwaida tana cikin filin dan amare sun taso take filin ya cakume da kida da rawa
shiko Mall waje yayi dan jin idon sa yana Nema rubewa Zaidu wani abokinsa ne ya fashinci halinda yake ciki yabi bayansa sai da ya tambayar yasa shi amota ya koma ya shiga ciki Lawan ya kira yace ya kira Ruwaida Lawan da yaje yana ta yiwa Ruwaida magana yaga duk hankalinta baya jikinta dan dama ba rawa take ba neman ma hanyan zamewa take bata san inda zata ba dan ko ina jama a take gani kanta sai juyawa yake hannunta Lawan ya kama ya fara tafiya aiko binsa tayi kaman dama shi take jira
Lawan dube debe yafara amma bai ga Zaidu ba wayan sa yaciro yakirashi "YaZaid nafito da ita ban gan kaba.
ni ina ganika kayi dan tafiya zaka ga motan Mall da sojojin sa awajen.
"ok.
Yace tareda kashe wayan ya hango su
har suka karaso idon Ismail yana kan Ruwaida
Zaid ne yafito ya fude yana cewa"ran madam major ya dade bismillah ya budewa Ruwaida

kofan motan ta baya kallon Zaid tayi da alaman tambaya dan bata san saba Lawan yace "yazaidu ne abojin Yamall ga yayan ma yaciki"
Ruwaida asorace ta daga kanta ta kalli cikin motan gefen da aka bude din duk da bata ga fuskansa ba kamshin turaren sa ya sanar mata lalle shine dan bai dago kansa ba
Zaidu yace afuwa madam
Come in we want to talk to you zaidu yamata kwarjinin da baza ta iyayi masa gardama ba dan haka ta shiga "thanks. Yace tare da rufo kofan yayiwa wani soja alama da ya shiga mazaunin driver da sauri ko yashiga kawai mall jiyayi an jasu wayan sa ya zaro ya danna kira "meye haka ina kasa akaimu ."
wayan yana handsfree dan haka Ruwaida tanaji dariyan zaidu dayake cewa nasani nide kawai nayi temako ne."
"aikin banzai nace maka ina bukatane.? "ai ba sai kace ba malam idan bakaso sai ka kai kasuwa.
kashe waya yayi tare da jan tsaki duk k'amshin ta yacika motan yanzu haka wannan sojan dake driver ma yake jin k'amshin da sauri ya tsedashi ya fito sai lokacin yaga ashe ma sauran motocin sojojin ma suna binsu abaya suma cak suka tsaya yace wa wanda yake tukasu yakoma motan baya su koma kar subisa ya karbi Key fin ya shika azabure yaja motan har Ruwaida tana kifawa basu jima suna tafiya ba yayi parking akofar wani gida bashida wani girma sosai da kansa ya bude get din ya shiga da motan ko kallon inda take bai yiba "yashige ciki acikin motan tacigaba da zama har ta gaji ta kwanta bata san tsawon lokacin data dauka tana bacci ba farkawa tayi taji kamar ana kiraye kirayen sallah
Lalle Mall anan ya barta ta kwana gabanta ne yafadi tunawa da batayi tsallan i'shai ba ahankali ta fito tana jujuya wuyanta dan taji yana mata ciwo saboda yanda ta takura akwanciyar parlour ne babba sosai amma kamar ba d'akuna aciki sosai dan kofa daya tagani ga wayoyinsa da kayanda yacire a kujera ahankali ta karasa kofan motsin ruwa taji wanda ya tambayar mata da bathroom ne ba Bedroom bane
Juyawa tayi tana Kalle kalle to ina dakunan gidan wane irin kurman gidane afili tace "wannan de ba complete house bane. ..
jitayi an bode kofa juyawa tayi ta kalleshi daga sai dan boxers kansa a k'asa hannusa daya dafe da goshinsa ahankali yake takawa da alama de kamar bashida kuzari k'asa k'asa take kallon sa har ya k'arasa ya zauna akujera itama shiga tayi toilet din bawani kayan wanka a ciki k'aramin nema sosai bayin dauro alwala tayi ta fito Ayanda ta barshi ahaka ta samesa dankwalin da aka mata nadi shi taware ta yafa amma bashida girma dan hannuta duk abude rigansa ya dauka ya cilla mata yace "kiyafa akai tako ji dadin hakan ta gabatar da ishai ta zauna tana issitigfari bajimawa ma aka kira sallah da sauri ta gabatar da sallah dan ta bashi rigansa shima yayi amma tana juyowa tasamu yasa dogon wandon sa da singlet yana sallah zama tayi tana tilawan Qur ani kamar yanda tasaba har saida ta gabatar da walha ta dan juyo kadan kwance ta gansa akan dogon kujera ya nade hannunsa a k'erjinsa idonsa abude yana kallon sama tashi tayi ta k'arasa inda yake ta durkusa daga k'asa muryanta na rawa tace "Yaya ina kwana?."
bai juyo ba yace "kina lafiya?
itama bata amsa ba sai sake jefa masa wani tambayar ma da tayi tace "Yaya ba kajin dadine?
"Eh.

Ayya Yaya kasha magani mana kakira doctor sorry inbaka wayan kane?.
duk ta jera masa tambayar
"nace miki banida lafiya ne cewa nayi bana jin dadi rashin din dadin rayuwa daban rashin lafiya daban lafiya kad'ai Dr keda maganin rashin jindadin rayuwa k'addara ce daga Allah Aysha."
sosai ta tausaya masa tace "yaya me damuwarka?
mek'ewa yayi zaune yana kallon ta yace "kece kece Humaira bakya son nayi farin ciki baki damu dani ba Allah ya haliceni mutum me kishi bazan iya daukan Irin..... " dakatar dashi tayi yaya
"na yarda ni damuwa ce awajen ka nasan ban kyau ta maka ba amma yaya Kai ma kayarda k'addarane amma ka kasa daukan sa yaya duk matakin ta zaka dauka akaina ka dauka ciki harda mai maita min dukan da kamin amma dan Allah karka dauki matakin rabuwa dani wllh ina maka son da ba kowacce mace zatayiwa mijin taba kabani daman k'arshe zan yaye maka dukkan damuwarka zan saka ka farin cikin da baka taba jin sa aduniyar ma aurata ba zan kare maka marta banka...
sulalewa yayi ya sauko shima jawota yayi jikinsa da sauri tabi jikinsa tayi lif tana jin yanda k'irjinsa yake bugawa
yace "Aisha nayi zaton hakan ada nazaci kin tuba zaki karemin mutumcina amma daren jiya kinsake nunamin ba haka bane baki janza a Ruwaida abasu kalan da ake.....

Toshi masa baki tayi da hannuta tace "ai nace ka bani daman k'arshe zakayi mamaki wllh jiyan ma takurani sukayi amma gaba ba biki ba kome ake ayanda kake so ahaka zaka sameni."
"Aisha idan kika koma Ruwaidata ta asali me shiga ta kamala kamar ranan dana fara ganinki shine zaki gyara duniyata ina sonki tun randa na fara dasa idona akanki akofar gidan ku nida matawalle soyayyar ki yabani wahala shawon shekaru 7 aranan nagan ki da shigan da nafiso arayuwa ta ".

murmushi tayi tace "yaya kaima kana yawan tuna wannan ranan Ashe nima haka amma nafi tuna rana ta biyu da kabini Super market ka sameni
kacemin *matar Ismail* nace maka yaushe nace ina sonka zaka cemin matar ka sai kacemin ai kaima baka ce kana sona ba na adana soyayyata sai bayan aure domin *AMFANIN SOYAYYA AURE*
Ina yawan tuna kalmannan araina tabbas *AMFANIN SOYAYYA AURE* duk soyayyar da ba ayi aure ba babu amfani.
" haka ne *INDON MATA*. cusa kanta tasake yi sosai yaya dama kana sona.
"seta fuskanta yayi dai dai nasa yace aini tunda na dauki so ban ta ba ajiye shiba kullum ina d'awai niya dashi so wahala ne."
fusgewa tayi ta koma gefe tana turo baki

wara manyan idonsa yayi da alaman tambaya tace "ai na manta zan fasa sonka.
"saboda me my hanta?
turo baki yayi tace
"bayan da aka daura mana aure fada kayi tayi wai gwara a aura maka kuturwa makahuwa gurguwa Kai gwara Iya Salmai ahan a Aura maka ni."

" kai kai ni Ilu yaushe akayi hakan inji wa?."
"anyi mana ai agaban su Farida akayi kullum suna tsokanana....

*Tofa ruwaidan hajja ce tazo ta jone da miji ina alk'awarin da kika daukawa hajja* 😂

B jattko
[9/17, 11:25 AM] Batul Adam Jattako: AMFANIN SOYAYYA*
*aure*

(aure)

*NA*

*BATUL ADAM JATTKO*

28

zaune yake abakin gadon  idon sa akan fuskanta wanda dagani baccin bana dadi bane shi yama akayi hakan ta faru meyasa da bai samu Ruwaidan ba bai kira wani yace ya fasa zuwa malesiya ba da bai jefa mutane dayawa cikin k'unci ba ciki harda abin son da takusa rasa ranta saboda rashin kulawansa hannuta da yake cikin nasa ya matse har yanzu da zafi zafin yaji yana ratsa shi shima zazzabin yake ji dan yanda yasha fada agunsu Abba bai taba ganin b'acin ransu haka ba duk jijiyoyin kasa yafito
yanda ya matse hannu sai yaji tayi motsi da hannun ahankali ya furta "Ruwaidaaaa. rawa yaga idonta yanayi juyowa yayi ya kalli mutanen dakin yana murmushi yace "Ummi tashi zatayi.
Hajja tace "yanzu fa  mu akace mufita muna damunta Kai kasa ta agaba kana surutu duk wa ya janyo.?
Abban Ruwaida ne yace "Hajja mufita kamar yanda Dr yace zata iya barkawa kowane irin lokaci amfison kuma idan ta farka ta samu nusuwa abar mijin nata kusa da ita zata fi samun nusuwa."
Hajja tace "aiko tashi zaiyi mufita tare ina wani nusuwa tareda wannan mijin ko fa wata batayi da kwanciya a asbitin nan saboda dukan da ya mata kuma gashi yanzu ga abinda yasake janyowa tashi maza mufita nace tashi."
Baba haruna ne yace Ismaila tashi mufita ya mek'e yaji tasake rike hannunsa juyowa yayi yana kallon ta ahankali take bude idon ta tsayar dashi akan sa cikin azama ta mek'e zaune shima

zaman yayi hannu ta takai habarsa tana jujjuya fuskansa tace "ya ismail kaine dama nace musu baka mutu ba nasan baza ka mutu ka barni ba.  murmushi kawai yake mata bai iya furta komai ba sai da ta gama cikin tattausan murya yace "sorry  please... awani irin zafafe ta fado jikinsa ko kula da mutanen dake 'dakin batayi ba
Hajja ce tayi gyaran murya zatayi magana Abban Ruwaida yaja hannuta yana cewa" Hajja kinji abin da doctor yace ai idan ta tashi amata abin da hankalinta zai Kwanta kodan saboda abinda yake cikinta..
yajata suka fita sauran mutanen ma suka fita kowa da murmushi afuskan sa
ahankali yaraba jikinsa da nata yana kwantar da ita ahankali amma sai taki kwanciya tace yaya gida.
''Eh zamuje gida
"Yaya meya sa akace ka mutu.?
saboda jirgin da ake tunanin ina ciki yayi hasari amma ni bana ciki saboda nafasa zuwa malesiyan amma sai bayan mun gama waya dake aka kirani zamuyi meeting na gaggawa a Lagos kuma dole sai dani dama nayi tafiyar ne batare da neman izinin office ba shine nasamu jirgin Itopia a itopia akwai jigrin da zai zo Lagos atake shine ban samu lokacin kira ba nama kashe wayan saboda Alfa zai damu da rashi karasawa ta kuma ina sauka a Lagos lokacin meeting yayi shine ban kunna waya taba tun muna meeting room labari yazo wai nayi accident kinji yanda abin yafaru amma bazan mutu ba har sai nayi irin ajiyan nan so 20 sweet gani da iya buga wasa wannan bugu daya Yayi maganan yana laluman cikinta yana shafawa."
ajiyan zuciya ta sauke tace "Allah sarki Allah yajikan musulmin da suka rasa ransu yah amma meye ka buga bugu daya?
Murmushi yayi yana shafa cikin nata yace ammm ba yanzu zan gaya miki ba sai mun koma gida zan hada miki da kyautan First Night ...  wani irin daure fuska tayi tareda banka masa Harare har yana rike kunnensa alaman tuba
tace bana son kyautar first night din ai nagama cin kyautata tun aranan.
dariya yayi dan yaga no ta gatsene ko gori akan dukan da yayi mata ranan
yace ah ah nide baza a hanani kyautar da nayi niyya ba tunda ance yaba kyauta tukuiwuci to tunkafin nayi kyautan naci tukuwicin sa kin ganshi ya karashe maganan yana shafa mata ciki.
ture hannusa tayi tace "Allah ko kullum kake bani kyautan so goma bazan dena maka gorin na first night ba har karshe rayuwata sannan ko kullum kake kawomin kaza irin na daren farko to bazan fasa maka gorin saba dan kaji."
dafe goshin sa yayi da hannu irin ya shiga ukku yana girgiza kai bude kofa sukaji atare suka waiga doctor Salim ne yana murmushi yace madam kin tashi.?
harara Ismail ya banka masa yace "ka bamu sallama malam."
ank'i abaka sallaman ban sanka ba kai ka kawo tane."
daure fuska yayi ba alaman wasa yace "malam kafita kasan de matar aure ce ka shego ba knocking.
Doctor bay kulashi ba yajuyo yana kallon Ruwaida yace Aisha yanzu meyake damunki.?
sake sunkuyar da kanta tayi cikin kunya tace ba komai."
dan duk abokan Ismail kunyarsu take ji
murmushi yayi yace "ok duk abinda ki kaji kiyi saurin sanar dani koda ta wayane ki kula da kanki sosai muyi sa a cikin bamuyi Loosing din sa ba congregation. sake sun kuyar da kanta tayi

juyowa doctor yayi ya dafa kafadun Mall yana sakar masa murmushi yace "congregation my friend.
Mall yace "thanks Dr. Salim yace noot thanks ba kodiya a tsakanin mu."
Mall yace yanzu zamu iya tafiya."?
zaku iya mana amma fa dan madam nayi."
Mall yace aje de hakan ma nagode." Dr yana fita ya matso sosai jikinta yace "my mata yanzu fa gidan mu zamu wuce kar ki ba da fuskan zama a part din ummi balle wannan tsohuwar tasamu dama kinji."
gyada masa kai tayi yace" Yawwa mejin maganata.
"zaki iya tashi ko na 'dagaki. gyara shijab dinta tayi tana sauko da kafafunta tare da mekewa gaba daya amma tayi luuu zata fadi dan mugun ciwo kanta yake mata ga rashi 'karfin jiki "subbahalalla. yace tareda saurin tareta komawa yayi da ita bakin gadon ya zaunar da ita a cinyarsa yana tambayar ta me yake damunta ahankali tace "hajijiya da bacci.
"Sorry why did you say nothing to Dr? bari na kira shi yafara shirin zaro wayansa tace "ah ah nide gida."
bai yi musu ba cak yamek'e da ita yayi waje a parlour ya samesu mutane sun ragu sosai su abba ma duk sun tafi sai de Allah ya ta'kaita hajja da ta kasa ta tsare gengedi take bata ga fitowar Ismail da ruwaida ba mall yana fita a packing space bai saurari dan dazon sojojin da suke ta faman sara masa da bashi waje ba Yayi inda yaga Khalifa jikin motan sa yace "khall muje ko' Khalifa da idon sa yana kan waya ya d'ago da sauri yana cewa "ok yaya ya mude masa baya ahankali ya kwantar ta bude idon ta tayi cike da banci amma ta sake rufewa har bacci ya dauketa ahiga gefinta yayi Khalifa da zai ja giyan motan tayi wani irin yunkurin gaba zuwa baya hakan yasa Ruwaida ta bude ido da sauri alaman ta dan tsorata
"kai baka da hankali ne mehaka.?"
"Sorry yah. tsaki yaja tareda yin kwafa kafin Khalifa Yayi gaba har motan sojojin sun sa nasa a tsakiya amma su kunna jiniya ba sun san Mall bayaso musamman ahalin da yake ciki Hajja da aka tada ta atashi atafi tace ina ruwaida akace anyi gaba da ita fada tayi tayi shiyasa Abban Ruwaida yajata Motan da yake ciki ahe wayo yamata dan hanya suka janza zuwa hanyan kaduna amma dayake tana da saurin bacci amota kafin sufita akano har bacci ya daukote sai can ta tashi ta misisika ido tace
"Muk'ddam yana ganmu a jeji ba gidan su hjy Ruwayya za zamu ba."
mumushi Abba Yayi yace kiyi hakuri Umma kafin mu karasa anguwar aka kirani da gaggawa a kaduna."
"kaduna kadunan uwar ka meyasa baka saukeni ba Alhaji kasuwa tafi gida"
"Hajja kiyi hakuri banason tadaki kina bacci ne."
"baccin me kaide kawai baka damu da iyalinka ba sai kasuwa narasa me kake nema aduniya. haka ta karaci masifan ta da ga karshe ta rufe da gobe sai ta komo Kano Abba de bai ce komai ba dan yasan inde yana gari zai san yanda yayi ya hanata zuwa dan yau ta bashi kunya komai yazo bakinta sake shi take
*wai dan ma baka ga tijjaran ta na ranan da Mall yayi dukan first night ba*

Ismail suna karasawa gidan sa ya wuce da ita yajuyo yacewa "Khalifa kace yaran nan su tafi bakin babban get.

sojoji kenan
zai dauki Ruwaida tace "ah ah zan iya."
OK yace amma tana zararo khafar ta yaga ba takalmi kafin ta Kai kafan k'asa ya shureta sai cikin gida har sama a bed ya sauke ta yace "me zaki ci kisha magani."
cikin shagwaba tace "abincin Hamrah." cikin faduwar
gaba Mall yace "Kai ina my sall."? dan bai ganshi a asbiti ba

Ruwaida tace "ban sani ba.
"ko kinsan ana bani labarin abin da yafaru da keda Ummi da sahal na kawo a raina ko kowa ya jure rashina ban daku ukkun nan na sani duk inda Sall dina yake ba lafiya yanzu bari narage kayan jikina na watsa ruwa na nemi dan uwa ga waya ki kira Hamrah ta aiko abincin" karba tayi tana sa number Hamran aka dan tasan bashi da shi
shikuma ya zauna kunce igiyar takamin sa
Hamra tana dagawa Ruwaida tace "tawan danyen kifi nake son ki damafin karfasa yaji tafarnuwa bana son yayi yaji kuma..
"tom uwata ina jinyar mijin nawa wanda sana dinsa mijinki ko tambayar ya jikin sa bakiyi ba shima wanda Yayi jinyar dan shi yana zuwa ai keda ya yasan dake wajenki ya wuce..
cikin sanyin murya Ruwaida ta katseta da cewa "haba dan Allah me yasamu Yasall din?
Hamrah tsaki tayi tare da kashe wayan
Mall da duk yaji abinda Hamrah tace ai bashiri ya mek'e ya fasa cire kakin sojon nasa ma ahaka yace mata excuse me ko knocking bayyi ba ya bude yashiga tsid kamar ba mutum agidan dan dama Sahal bameson hayaniya bane
da sauri hamrah take taka stairs din zata sauko dago kai da zatayi taga mutum a saye turus ta tsaya kamar zataja baya dan ita tsoron Mall take ji musamman idan ta ganshi cikin kaki ga kuma bata taba ganin ya shigo musu gida ba ganin tayi shiru yayi murmushi yace "madam sannu da gida me gidan fa.?
Hamrah wani ban bara kwai taji dan magana bai taba shiga tsakanin su ba cikin in ina tace "yana sama.
"ko zan iya shiga.
gyad'a masa kai tayi tareda karasa saukowa dan ta bashi hanya tace "room 2.
"thanks.
yace tare da wucewa
ita ma tayi kicin dan daurawa Ruwaida dahuwar ahankali yamurda kofan ya shiga kudun- dune ya hangoshi a tsakiyar gado fisge blanket yayi da karfi daga shi sai gajeren wando da sauri sahal ya bude ido yana kallon Mall yamek'e zaune "me haka zaka shigowa mutane har 'dakin aure malam ko kadauka irin da damuke kwana tare ne.?
dariya Mall yayi tare da fadawa gadon da tsalle yana cewa "wllh har katuno min da da ina mugun missing na numfashin ka my friends.
binsa da kallo sahal yayi yana gani tsansan farin cikin da yajima bai ganshi a ciki ba ya tabe baki yace' kagama ruda kowa a family kai kana cikin farin ciki abinka."
Mall yace "ina cikin farin cikin ne ai kuma ko yau na mutu ina da magaji nan da dan watanni kad'an."
"Au haka ma kace" cikin

dariya yace" ai wllh  dariya kuka bani duk yawan mu agidan nan dan anrasa mutum daya sai arikice kaga ko yanda na tadda gidan nan.?
Sahal da sauri ya rungumo Mall sosai suka  suka cukumo juna "bro ahe haka jin labarin mutuwa yake gaskiya mun sa kankancewa rayuwa bayan bata da tabbas wannan abinda yafaru a familyn yana nan zuwa ko amu ko a iyayen mu akowane lokaci Ismail banyi bakin cikin faruwar wannan abin ba dan yasa muntuno da abinda muka shagala dashi kuma mutuwa wajibine dole mu sa hakan aranmu.
Mall yace "hakane mutuwa akwai d'aci Allah kabamu nisan kwana me amfani.
sosai suka fara tattaunawa akan rayuwa
Sahal yace "yanzu tafiyan ka goben akwai kenan?
"Eh in sha Allah.
"ok bari nayi wanka.
yatsine fuska Mall yayi alaman ky'ama yace"wanka haba shiyasa nake jin warin Barbara k'azami malam.
yana maganan yana shinshina rigan jikinsa da saure sahal ya mek'e zai bisa yayi saurin ficewa a part dinsa
a parlour k'asa ya tadda yawanci yan matan gidan  sun baje sai cin Pepe soup  din kifin da hamrah ta dafa suke ana ta cin dariya ciki-ciki yayi sallama bai ko Kalli inda suke ba ya shige ciki hamrah ce tafara tashi tace "tunda kuka cinye mata ai sai kuje ku dafa mata wani dan anjima zataji yunwa." Hamida tace "tam aikam ba niba wllh kicking umm. haka duk suka zame sukayi gaba ita kuma Ruwaida tayi sama
zaune ta samesa abakin gadon kansa asunkuye   yadafe goshi da hannu 2 tayi sammanin zata samesa yana bathroom ko yana shirin cire kaya matsawa tayi dai-dai kafafunsa cikin sanyin ta tace "yaya ba zaka cire kakinnan ka watsa ruwa ba?
ahankali ya dago yana kama hannuta tana kallon kwayan idonsa taza da baya arasane "me yasameka ? kaga idonka kuwa yanda yayi jajir.?
Ruwaida wannan sojan da kuka gani ya shiga jirgin nan Fawwal Abdullah Mohammed ne abokinane dan Syria shima duba Alfa zaije.
Ruwaida tace" Allah humma gafurni walhamni Allah yaji k'ansa.
zama tayi ak'asa tasa hannunta tana kunce masa igiyar takallmin sa tana gaya masa kalamai masu dadi "haba sojana Fawwal fa yafika jin dadi ahanin yanzu yasamu riba 2 na sha hada da niyar ziyartan Marar lafiya ga kunan wuta in sha Allah muna kyautata masa rahama hannunsa ta kama ta mek'ar dashi bayan ta cire masa rigan sa na sama ta barshi dagashi sai singlet da dogon wando mak'e mata kafada yayi yana nuna mata bel dinsa
ita ma mak'e kafadan tayi tana tattare fuska yana murmushi yace "ahe bakya son nayi wankan kenan.?
''tom ba na cire rigan ba sauran ka k'arasa mana.
mak'emata kafada yayi yana shagobe fuska yanda takeyi yace "ke zaki karasa cire su. tace "ni kam ban iya ba.
yace
" wayafiki iyawa irin yanda ki kamin a sabon feji fa.
turo baki tayi tace "na manta.
"ok zona tunamiki.

Matsawa yayi jikinta yayi hugging dinta yana zipping riganta Before she knows her gown is down batayi ko matsi ba balle ta hana shi haka yamata zir yana jujjjuyata yace "haka nake sonki min.
idonta ta sake rufewa tana turo baki
ganin zata bata masa lokacin yasa yakamo hannunta ya daura akan bel din yace "ban san Aisha da sab'awa umarnin miji ba fa.
jin haka da sauri ta bude idonta ta sauke akan hannunsa da nata da yake ahade akan bel din ahankali tafara kiciniyar bude wa amma ta kasa dan bel ne na soja sai su ganin ta kasa yasa yace "zan baki satan amsa amma fa na yau kad'ai
bai dauke hannu nata ba ya shiga balle wa idon ta akan yanda yake yi shikuma idon sa akanta yana gama budewan ko ya janye hannun sa dolenta ita tayi zipping din wandon zuwa k'asa daga shi sai boxer jin tayi shiru yasa yace" cigaba mana. " na cire fa. "wannan fa. ya nuna mata boxers kiyi aikin ki nifa tabona nake kallo yayi maganan idonsa akan kirjinta bin inda yake kallo tayi ai bama tabo kadai yake kallo ba wani irin kunya taji kamar yau ta fara tsayawa da namiji a haka ita Ruwaida da zatayi zir agaban namijin bariki tayi ta kwasan rawa ne yau agaban mijin aurenta ta kasa lalle aure rahama ne akwai kunya da karramawa na musamman acikin aure "kinsan me ai ko kwana zamuyi anan sai kincire gajeran wandon nan umarni ne.
ahankali ta daura hannuta a kugunsa idon ta arufe ahaka taja sa k'asa da gangan yayi wani tangal tangal zai zube a k'asa da sauri ta bude idon tana tarosa amma sai da sukayi k'asa dukkansu dan yamata nauyi kafin yakai k'asa tayi mugun fadawa kirjinsa suka tafi atare da sauri ta mek'e zaune jin yana cewa "wash-wash.
"! Yaya kaji ciwo ne inane tayi maganan tana d'agosa amma ta kasa kugunsa ya dafe yana fitar da numfashi da sauri ta Kai hannuta wajen tana cewa "nan ne.? duk ta rikice yace "ah ah inda kika fadomin ne".
Cikin sa ta danna "nan yace "ah ah sake yin k'asa sosai. hannuta yana rawa takai har k'asa da cibiyar sa ta danna tace "n nan...
cikin wani irin muryar vibration yace "k'asansa dear.
zaro ido tayi cikin rawar murya tace "Allah yaya nafa kure ko ina kuma ni ban fada har canba. bazato taji yadaura hannunta akan aiko wani irin shocking taji har cikin kwakwalwar ta idonta cikin nashi da suka k'an k'ance sai yace "nanne yake min ciwo murzamin shi my Ruwa.
tana gama fashimtar me yake nufi ta zage ta fitar sa ahayyacin sa ba jimawa yasamu wani gam she -shen nusuwa bata reda yayi Sex da ita ba rungumota yayi yana sambatun sa mata albarka ita ko zuwa yanzu ta gane waye mijin nata romance Man ne wasanni yafi so fiye da saduwa Allah ya temaketa ta iyashi duk da tana bukatan saduwan musamman da yayi wasanni na motsa sha awa sosai da ita amma haka ta hakura dan ta koyawa kanta abinda yafi so kodan inganta soyayyar ta abaya ya goyata har cikin bathtub anan ma sai da suka sake shadewa agogon ban 'dakin ta kalla tana furta "assagfurlah ya kalli ankusa kiran magruba ko azahar banyi ba.
juyowa yayi yana kallon agogon yace "yaushe lokaci yaja haka nima banyi la asar ba. wankan tsarki zukayi me hade da alwala amma Alwala de agun sa yak'i dauruwa yasan kuma inde zai cigaba da kallon ta ahaka zai shekara bai kyauta ta alwalan ba
yace "fara fita in same ki da kaya ajikin ki saboda gudun kuskure.
dungurin kansa tayi tana dariya tace "kuskure na nawa kuma ai kagama kuskurewa."

yunkurawa yayi da niyar sake caf kota ta zille cije lebin sa na k'asa yayi tareda yin kwafa yana cewa "zan kamaki zakiga kuskure yarinya.
dariya take har ta karasa inda towel suke da sauri ta daura daya ta rufa daya ta fita sauri sauri take ta zaro doguwar riganta na sallah me hade da shijab fari tas tasa ajikinta ta bude wadroop din da take tunanin kayansa ne aciki dan sabone ada bata sansa adakin ba wannan shi ya tabbatar mata da yataro part dinta gaba daya jallabiya ta zaro masa ash colour da boxes baki gaban budubi taje tana fesawa rigan turare ya fito daure da towel sai faman d'igan ruwa yake ta kalleshi tace amma da kafito da towel na gogewa kaga yanzu kana sa kaya zai jike gashi masallaci zaka."
" su yan masallacin basu san ango bashida lokacin wanka ba.
girgiza kai tayi tana murmushi tana shirin tada ik'ama yace badan bakiyi la asar ba da na jamu zan fita sai nayi ishaa zan shigo kina bukatan wani abu ne.? tace "Eh.
"good Girl me kike so?.
jujjuya ido tayi kamar me tunani ta sauke akansa tace "biyan bashin kazan first night dina." dafe goshin sa yayi
"Wooo ni Samaila gori najiran ranan sa zakici kaza har uban sa zakara."
" nagode adawo lafiya Abu Mus'af.
" Mus 'af kai shi kike son yafara zuwa munsamu sabani ra ayi nikuma yara mata nake so dayawa dan yanzuma ina sa ran zuwan Khadeeja Ammi."
musmushi tayi tace
"to Allah yabawa meraso sa a yaku ma bamu masu albarka Yaya sai kazo" ta tada ik'ama
"Ameen"
ya furta yana fitowa Sahal ma yafito suka jera yana tsokanan sa har yafara kyallin angonci kode kode "kasanta de magulmaci kowa ma kamar kaine namamajo."
Sahal yace "na yarda da wannan sunan Baba waliyi muje.

"Ummi muyi sallama tun yanzu dan kafin ku tashi zamu wuce. "ok idan ka shiga katuro min da Ruwaidan kar ma kasa ran tafiya da ita dan da alaman cikin yana bata wahala.
"dan Allah Ummi kiyi hakuri Allah inde ba Aisha zan iya hakura da tafiyan dan ko naje hankalina bazai kwanta ba.
Ummi zatayi magana
daddy yace "ah ah Hajiya kibar yaran nan su huta Ismail ba yaro bane zai iya kulawa da iyalinsa yan da ya kamata ke ko kunya ba kyaji ita wanda kike dan ita tana baki kunya amma sai sake dagewa kike."
Ummi cikin fushi tace "ai bata san kanta bane halin kharajina ta kwaso na wauta macce sai kace ba macce ba."
dariya daddy yayi yace "hakan shine dai-dai ai matan yanzu sunyi arayuwa ga wayewa ga ilimi.
Ummi murtuke fuska tayi dan bata son taji yana yabon matan yanzun nan da yake yawan yi.
matsowa Ismail yayi kusa da ita ya durkusa "Ummi kidena 'bata ranki zan je na kawo miki Aisha har sai sanda kika yi ra ayi kika bani ita da kan ki nasan ke Uwace me adalci ga yaranta kuma meson farin cikin su zaki bani Aisha ko ba yau ba dan itace farin cikina nasan kinfi son farin ciki na fiye da komai uwa tagari ina alfahari dake Ummi ya k'arasa maganan yana hada hannusa da nata.

ajiyan zuciya Ummi ta sauk'e tafi kowa sanin halin Ismail inde yanason Abu to yasan duk hanyar da zaibi yayi nasara dan da bakin sa zai kashe mutum gyaran murya tayi tace "Ismail kai kanka sheda ne akan sonda bakeyiwa Kharajina tun kafin nasan tana raye ita kadai ta rage min ita nake kalla nace ga nawa bayan ku dana haifa acikina ina son kharajina sonda bansan iya kansa ba inason yaranta tamkar yanda nake sonku duk girman son da nake maka ayanzu idan nace ga wanda nafi so tsakanin ka da Ruwaida nayi karya
inason ka rik'e Ruwaida da kyau nasan kai adaline kuma me biyayya Allah yasa alkairi cikin rayuwanku ya baka ikon rike ta da kyautatawa yasa albarka cikin rayuwan ku. cikin wani irin farin ciki yace
"nagode Ummi kin sauk'e duk wani hakkin ki arayuwa ta Ummi duk wani abinda uwa take yiwa d'ah kinyimin Allah yabani ikon sauke nawa nauyin akanki Ummi namiki alk'awarin saka rayuwan Aisha cikin farin ciki bazakiyi nadaman bani ita ba in sha Allah."
Sosai suka masa nasiha me taba zuciya

*Bayan wata ukku*

saukowa take cikin wasu English wears na daukan hankali wani
mini siket iya rabin cinyar ta sai haf bes iya boob's dinta kawai ya rufe fuskanta ba walwala take saukowa a stairs din  kwance ta hangoshi bakin swimming pool cikin wani kujera na 'karfe daga shi sai three quarter ba riga gashin kirjin sa da yake dauke mata hankali dashi yayi wani irin kwanciya dan aruwa yafito dalilin kiransa da akayi a waya waya manne a kunnen sa  jin takun ta yasa yadago yana kallonta cikin murmushi yake nuna mata cinyar sa sai da tazo daf dashi da zauna abakin swarming full din ta zura 'kafanta cikin ruwan tana sake hade fuska
kwanciya Yayi akan  dogon kujeran karfe irin na bakin ruwan nan tareda da meko
'kafafun sa yana sake matsowa kusa da ita kafafuwan sa biyu yasa gefe da gefin hak'ark'arin ta har yasamu nasaran cusa kafatuwan sa duka biyi cikin yar rigan ta sarrafa kafafun nasa yake yanda yaso acikin rigan har ya samu nasaran tura rigan zuwa wuyanta yajima yana wayan kafin yayi sallama yataso zuwa inda take amma shi cikin ruwan ya shiga a tsakiyar kafafunta ya zauna tacikin ruwan yake kallon ta "haba sugarlips har yanzu fushin ne meyasa har yanzu kin kasa sabin halin mijinki mutum ne da baya daukan umarni ke kuma kina da son isa da son abi ra ayinki duk inda kikaga zaman tare yayi dadi to akwai sadaukarwa akan ra ayin wani.
"habibi amma kasan kullum ni nake sadaukarda nawa ra ayin awannan karan na nemi alfarma ne kuma ai watanin ukku kace zamuyi yanzu kuma har munshiga na 4 kamin adalci mana yaza ayi yau ana sunan aunty Ayya guda amma bani aciki .Allah yabata kyauta na yara biyu amma ni dasu sai awaya aik.....
maganan tane ya ma'kale tana ware idon ta akan wayan sa dayake ta zooming din hoton wata kyakkyawar jaririya tana ganin sa yakai wayan bajinsa dai dai goshin jaririyar ya dinga sakarwa kiss yana murmushi tana kallon sa yajuwo yadaura wayan a cikinta yace "Ammi tashi ki gaisa da best sister friend din ki Fhutteeatul Khairi ki san ta tun kafin kizo duniya dan inaso kuyi zumunci da abota fiye da yanda mu iyayenku mukayi kingan ta kyakkyawa tabiyo walwala kema walwalan zaki bi karki biyomu nida umman ki kikode dayawa nafi sonki da duhu
best daughter  aiko kamar cikin yana ji yayi wani irin motsi "Yawwa kinji ai my Ammi yakai bakin sa kinda yake motsin ya dinka Kinss din wajen yana surutansa

Ruwaida bakinta ne kawai yake rawa ta kasa furta koda kalma daya shiko ko ajikinsa ya juya yana daura hotunan yarinyar adukka kafar sa ta yada zumunta yanzu kam ta gama yarda jaririyar tana da muhimmanci awajen Ismail dan ba karamin abu yake daurawa media ba kai ko hoto ne awayan sa to me mahimmanci ne aiko ko second 10  ba ayi ba aka fara masa fatan alkairi ahankali ta sauke kansa acinyar ta zata tashi ya kamo hannuta yana ganin yanda idonta ya ciko da kwallah yace " stop crying mana sugarlips abincin zuciyata lafiyar gangan jikina my....
"nikam kayi shurunka kawai ba abinda zaka cemin har Hamrah ta haifu ban sani ba bani da matsayin da zaka kayamin sai 'yar ka da take ciki ka hana narike waya kuma ba komai kake gayamin ba.
"ohoo sorry dear naga kina fushine kuma wannan abune na farin ciki shine nabari sai kindan sauko na gaya miki."
"kari 'ke kayanka ni bana farin ciki tayi maganan tana fisge hannunta tayi ciki shima mek'ewa yayi yana cewa Ruwa rigima

*A maiduguri*  kuwa yau ake sunan twins  din Ayya Muhammed da Ismail wanda daya yaci sunan Ismail daya kuma duno marikin Ayya

*fadan shagalin sunan bata lokacine kashi bamuda lokacin kuyi hakuri ban cika muku alkawarin gamawa a 28 ba  kunga de yanda labarin yake tafiya wani wajen ma ba a taboshi ba abin yayi yawa labarin mutum 3 sai ahankali yanzu de zamu tsaya a 30 ko wanne labari yazauna amatsayin 10 gp kenan hakan ma an tak'aita*

08062383027
[9/17, 11:25 AM] Batul Adam Jattako: *AMFANIN SOYAYYA*

*NA*

*BATUL ADAM JATTKO*

Masha Allah
Zainab Mustapha
Mmn sadik marubuciyar Mutum a fuska
Allah yaraya mana Aliyu haidar

*27*

"dawo my sweet baby ai awannan lokacin borin dadi ne ya sani nafadi hakan dama nasara yanda zanyi nafito na nuna ina son auren ki bazato sai gashi ance an daura sukuma muna fukan da suke sokanan naki kiman ta dasu mijinki yafi nasu ne kinfi su babban kamu hassada ne.
jowota yayi ya daura kanta akafafuwansa yace "kiyi bacci nasan kwanciyar takura kikayi acikin

motan baki samu baccin kirki ba bajimawa baccin ya dauketa wayansa ya janyo ya dauka ya kira Lawan sai daya kusa tsinkewa ya dauka muryansa da alama abacci ya tashi yace "Yaya ina kwana"?
"bakayi sallah bako ?
shiru lawan yayi dan ko sai wajen 3 na dare suka kwanda saboda shidiman biki bayyin ba
"yaya yanzu zanyi."
"to idan ka idar kai da Kharajina kuje gidana ku hado mana duk kayan da zamu bukata na sawa nida Aisha ka kawonin wannan gidan da nake Meeting na sabon feji.
yana gama ba da umarnin ya kashe wayan yana kallon yanda take sauke numfashi ahankali shima ya kwantar da kansa ajikin kujera yana cikin bacci yaji Knocking ya bude ido har yanzu baccin take akan kafatuwan nasa yana motsawa zata iya tashi kuma yasan Lawan ne wayan sa ya dauka yakirashi yace "shigo." Lawan yana shigowa yaga yanda Ruwaida tayi wani kane kane acinyar Ismail tsunkuyar da kansa yayi har ya karasa meka masa kayan yayi tareda cewa "Yaya
good morning kansa asunkuye zai juya yaji yace "tsaya na duba kayan zauna mana ya nuna masa kujeran kusa dashi zaman yayi tareda sake gaisheshi "lafiya ya gidan Ummi bata nemi Ruwaida ba?
Lawan ya d'ago yana kallon Mall yace "ta nemeta tun awajen dinner amma ni ta tambaya dan taga sanda nafita da ita nace tana wajenka.
"OK meta ce?
"neman ka tayi tayi a waya switch off .
"ok inaso kaje kayimin bucking na ticket
Germany nida ita idan baka samu
direct Germany  kayiwa manager magana zai dubo maka k'asan da za asamu flight na Germany ayau ."
daga jin yanda yake maganan a hankali kamar ba shima lawan ya gane bayason ya tashi matar sane."
Lawan yamek'e yana gy'ada Kai har yadanyi taku biyi Mall yasake cewa amm kasamo mana abinda zamuyi Breakfast .
"ok. yace  Lawan
yana fita yasamu Khalifa da yabari amota yana ihoo yace kai khal dama boss dinnan haka yake ashe duk yanda muke tsoron sa kamar malaika idan yashiga daga ciki wllh bawa ma yafishi kai aure yayi na yarda yana gyara mutum kaga yanda man dinnan yake wani magana silent ba wannan dakiyar." "
kai dakata wai awannan akurkin gidan har wani abun Kaga anayi.?
kai gidan ne akurki amma rayuwar da ake ya girmi hakan".
ya kwashe komai ya gaya masa
Khalifa yace "shikenan shima yakoma Yasall shima kaga yanda yake da hamrah agaba kowa.
Lawan ya tada motan yana cewa mu sai munyi wanda yafi nasu musamman idan nasamu Yagana wannan yarinyar da Aunty Ayya tazo da ita.

Itako Ruwaida tajima da tashi tun knocking din lawan kunya ne ya hanata tashi ayanda yaga idon ta yana motsi yasan ba bacci take ba yatsan sa biyu yasa ya danne mata kofofin hanci ta

dena nunfashi aiko sai ta  bude baki tana jan nunfashin ta baki ahankali ya ja bakinsa dai dai idon ta ya zuba mata yawun da ya tara aduka idon da sauri ta bude idon yawun ya shige mata ido
tayi saurin jan singlet din jikinsa tana gogewa tace "yaya meye haka"?
yace "maganin me baccin k'arya mana haka na keyiwa maina kange abokina san da wuya tayi wuya a school idan yagaji sai yayi baccin karya."
Ruwaida tana goge idon tace "general  Maina abokinka ne? "Eh kinsan sane." Eh ina ganin sa a TV kuma last week naga karramawan da aka masa na sanin makamin aiki duk shine me mafi k'an k'antan shekaru acikin su sai de nayi mamakin da ake tambayar iyalin sa yayi shiru sannan fuskan sa ya canza."
shima Mall canzawan yayi tareda nin shiru

Yaya ko bashida mata ne?
My wife kibar zancen yana da tada hankali rikicine a familyn su sosai da wani brother dinsa *Ismail maina kange il*  abin ba dadin ji kawai ki sashi a adua friend dina ne wllh.
"To yaya ka gaya min mana me ya ke faruwa."
girgiza kansa yayi alaman bazai iya fada ba

NIKO ZAN KAWO MUKU LABARIN *KANGE FAMILY* KO BA YANZU BA IN SHA ALLAH
labarin me taken *ANAYI DA KAI..*  yafi ba ayi da kai kana sarki amaida ka me anguwa 👌🏼

